# COURSE GUIDE

**NATIONAL OPEN UNIVERSITY**

**DEPARTMENT OF LANGUAGES**

**FACULTY OF ARTS**

**Programme: B.A HAUSA**

**COURSE CODE & TITLE:**

**HAU 212: SYNTAX OF HAUSA 1**

**Course Writer:** **Professor Hafizu Miko Yakasai**

**Course Editor:** **Professor Salisu Ahmed Yakasai**

# HAU 212: NAHAWUN HAUSA 1

## Gabatarwa (Introduction)

Wannan darasi na HAU 212, yana da muhimmanci wajen koyo da nazarin Hausa, musamman darasin da ya shafi nahawu da ya kevanta ga Hausa. Darasin ya kawo cikakken bayanin yadda zubi tsarin nahawun Hausa yake. Har ila yau, darasin ya tavo batutuwan da suka danganci li'irabin jimlolin Hausa. Darasin ya fito da bayanin nahawun Hausa daki-daki.

An gabatar da darasin bisa tsari na rukuni-rukuni kuma kowane rukuni ya qunshi kashi- kashi na batutuwa daban-daban da suka danganci nahawun Hausa da li'irabinsa. A cikin darasin an zo da cikakken bayani kan dukkan zubi da tsarin kwas xin ta yadda xalibi zai naqalce shi ba tare da wata wahala ba. A qarshen kowane kashi an zo da tambayoyin auna fahimta kan batutuwan da aka gabatar qarqashin kowane kashi. Fasalin tambayoyin da xalibi zai gani domin nazari kafin zuwan jarrabawa a qarshen karatu nuni suke yi kan abubuwan da aka koya wa xalibi a wannan kashi. Haka kuma an samar da dama da xalibi zai iya tuntuvar malami domin qarin haske a duk lokacin da wani abu ya shige duhu.

## Manufar Kwas (Course Aim)

Domin kyautata karatu da koyarwa kowane kashi yana da tasa manufa bayan babbar manufar kwas xin ta gaba xaya da aka zo da ita a farkon darasi. Ke nan abin da xalibi zai yi domin sauqaqa karatunsa shi ne ya karanci kowace manufa da take haxe da kowane kashi na darasi domin gane ciki da wajen darasin, ba tare da an samu matsala ba.

Idan xalibi ya kula da kyau zai ga cewa manyan darussan da ke tattare da wannan kwas suna da yawa, sai dai za a iya taqaita su kamar haka:

- Me ake nufi da Nahawu?
- Rukunonin Nahawun Hausa
- Zubi da Tsarin Jimla A Nahawun Hausa
- Jimla Mai Aikatau da maras aikatau
- Lokutan Hausa
- Li’irabin Jimlar Hausa

**Yadda Za A Nazarci Kwas (Working through the Course)**

Domin ganin an fahimci wannan darasi da kyau an tsara darasin ta yadda xalibi zai iya jan ragamar karatunsa ba tare da ya fuskanci wata matsala ba. An dai rarraba kwas xin zuwa rukuni-rukuni da suke qunshe da kashe-kashe masu dangantaka da juna, kuma kowane kashi an gabatar da shi yadda xalibi zai ga dangantakarsa da xan’uwansa da ke biye. Saboda haka fahimtar darasin zai biyo karatun ta-natsu da xalibi zai yi wa darasin, ya kuma auna fahimtar xalibi ta yin amfani da tambayoyin da aka zo da su a qarshen darasi. Da yake kuma akwai aikin jinga da malami zai dinga bayarwa bayan kowane kashi na kwas ko darasi, xalibi zai samu damar ganin fasalin yadda jarabawa za ta kasance in an gama darasin baki xaya ba tare da ya dogara da malami ba a wannan lokaci. Ana fatan a kammala kwas xin cikin mako 15, wato kowane kashi a cikin mako guda.

Daga qarshe xalibi ya sani cewa idan yana nazarin kwas xin, malaman da zai riqa tuntuva ba koyaushe za su kasance tare ba, saboda haka sai xalibi ya yi jadawalin karatunsa ya dace da kowane kashi na karatu, ya kuma dinga ziyara da leqa abubuwan da malami ya sanar da shi domin qarin nazari da faxaxa sani da kuma qarin haske.

Me ya kamata xalibi ya mayar da hankali a kai a lokacin gabatar da wannan darasi? Xalibi ya tabbata ya fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan darasi ko kwas yana da rukuni 3 da kashi 14.
2. A wannan kwas rukuni na 1 yana xauke da kashi 5, rukuni na 2 yana xauke da kashi 5, sai kuma rukuni na 3 yana xauke da kashi 4. Gaba xaya ana da kashi 14.
3. Kowane kashi yana da vangaren auna fahimta.
4. Kowane kashi na darasi yana da jingar da za a yi.
5. Kowane darasi ko kashi yana tafe da manazarta da wasu ayyukan don qara nazari.

**Kashe-Kashen Darasi / Kwas (Study Units)**

A wannan kwas akwai rukuni 3 da kuma kashi 14, kowane kashi yana a matsayin mako guda ne na darasi, ke nan za a kammala shi cikin mako 15. Ana kuma fatan a amsa tambayoyin auna fahimta a qarshen kowane kashi, daga qarshe kuma a amsa tambayoyi na jinga don ganin ko darasin ya zaunu da kyau.

Domin kyautata karatun kwas xin an haxa da jerin littattafan da aka duba da wasu ayyukan da za a iya cewa suna da muhimmanci ga wannan kwasa xin, za su qara haske fiye da qima. Neman waxannan littattafai da wasu irin sa a laburare zai inganta nazari da fahimtar kwas yadda ya kamata. Ke nan a shiga gonar xakin karatu a gida ko inda ake ajiye littattafai a kusa ko nesa zai inganta nazarin wannan kwas.

A kula da liqau da ake sa wa a cikin kowane kashin darasi, za su taimaka wajen qara haske na nazarin kwas xin baki xaya, sai dai a tabbata liqau xin suna aiki yadda ya kamata, kada a bari sai lokacin da ake buqatar su, a laluba a ga ko suna aiki ko ba su aiki, wato dai a gwada komai kafin qarshen kwas xin.

**Auna Fahimta (Assignment)**

Shi wannan kwas na tsarin da ba ruwanka da malaminka ne, ko na tafi-da-gidanka, shi ya sa ake jarraba fahimtar karatu ta hanyoyi UKU, hanya ta farko ita ce ta auna fahimta a qarshen kowane kashin darasi, sannan a zo da jinga da za a ba wa xalibi a qarshen kowane kashi, shi ma, sai daga qarshe a yi jarrabawar qarshen zangon karatu, wanda zai nuna an zo qarshen darasin.

Auna fahimtar da ake yi a qarshen kowane kashi za ta kasance qaramar jarrabawa ce, za ta zo da maki 30 daga cikin 100. Ke nan, ana buqatar xalibi ya amsa tambayoyi uku inda za a zavi 2 su kasance su ke xauke da maki 30, maki 15 ga kowace tambaya. Sauran maki 70 za su zo ne a jarrabawar qarshen kwas.

Jarrabawa dai kamar kullum za a gabatar da ita ne daga gida, ita ma ba a cikin aji ba, kuma za ta kasance ta Intanet ne, ke nan ilimin na'ura mai qwaqwalwa abu ne mai muhimmanci ga xalibi.

## JINGA (Tutor Marked Assignment)

Jingar aji tamkar gwajin jarrabawa ne ga xalibi, saboda haka amsa jingar da ke qarshen kowane kashin darasi zai ba wa xalibi damar fahimtar yadda jarrabawar qarshe za ta kasance. Yana da kyau xalibi ya mayar da hankali domin amsa irin samfurin waxannan tambayoyi, domin za su sauqaqa amsa tambayoyin jarrabawa a qarshen darasin baki xaya.

## Jarrabawar Qarshen Darasi (Final Examination and Grading)

Ita dai jarabawa ita ce hanyar da ake gane ko xalibi ya gane darasi ko kuma ya samu naqasu a wani vangare, saboda haka tana xauke da kaso mafi tsoka na 70 cikin 100. Ba wani dabo a cikin wannan fasali domin ana xauko samfurin jarrabawar ne daga tambayoyin da aka dinga turawa na auna fahimta da kuma jinga. Ke nan mayar da hankali wajen amsa waxannan tambayoyi a lokacin darasi zai rage zafin tambayoyin qarshen darasi.

**Ga fuskar yadda darasin zai kasance:**

**RUKUNI NA 1**

KASHI NA 1

3.1 Me Ake Nufi Da Nahawu?
3.1.1 Nahawu A Ilimin Kimiyyar Harshe
3.2 Dalilin Samuwar Nahawu A Harshe
3.3 Nahawun Hausa
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 2

3.1 Rukunonin Nahawun Hausa 1
3.1.1 Suna
3.1.2 Wakilin Suna
3.1.3 Harxaxxen Suna
3.1.4 Amsa-Kama
3.1.5 Sifa
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 3

3.1 Rukunonin Nahawun Hausa II
3.1.1 Aikatau
3.1.1.1 So-Karvau
3.1.1.2 Qi-Karvau
3.1.2 Bayanau
3.1.3 Sarqaqqiyar Nasaba
3.1.4 Ma'auni
3.1.5 'Yar Mallaka

4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 4

3.1 Ma'anar Jimla a Nahawu
3.2 Sassan Jimla
3.2.1 Yankin Suna
3.2.2 Yankin Bayani
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

**RUKUNI NA 2**

KASHI NA 1

3.1 Nau'in Jimla Mai Aikatau
3.1.1 Miqaqqiya
3.1.2 Korarriya
3.1.3 Qarfafau
3.1.4 Tambayau
3.1.5 Umurtau
3.1.6 Haxaxxiya
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 2

3.1 Nau'in Jimla Maras Aikatau
3.1.1 Dirkau
3.1.2 Tambayau

3.1.3 Nunau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 3

3.1 Tsarin Jimlar Hausa
3.1.1 Aikau + Aikatau + Karvau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 4

3.1 Ma'anar Qarfafawa
3.2 Ire-iren Qarfafawa
3.2.1 Qarfafawa Ta Jigo
3.2.2 Qarfafawa Kevantau
3.2.3 Qarfafawa Bambantau
3.2.4 Qarfafawa Rikixau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 5

3.1 Ma'anar Ganga
3.2 Ire-iren Ganga
3.2.1 Ganga Dogarau
3.2.2 Ganga Tsayayyiya
3.3 Matsayin Ganga A Nahawu
4.0 Kammalawa

5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

**RUKUNI NA 3**

KASHI NA 1

3.1 Ma'anar Lokaci
3.2 Lokutan Hausa 1
3.2.1 Shuxaxxen Lokaci Na I
3.2.2 Shuxaxxen Lokaci Na II
3.2.3 Lokaci Na Sabo
3.2.4 Lokaci Na Yanzu Na I
3.2.5 Lokaci Na Yanzu Na II
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

Kashi Na 2

3.1 Lokutan Hausa II
3.1.1 Lokaci Na Gaba Na I
3.1.2 Lokaci Na Gaba Na II
3.1.3 Umurtau / Wanin Lokaci
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 3

3.1 Ma'anar Li'irabi
3.1.1 Bishiyar Li'irabi
3.2 Li'irabin Jimla Mai Aikatau

4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

KASHI NA 4

3.1 Li’irabin Jimla II
3.1.1 Li’irabin Jimla Maras Aikatau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

# HAU 212: NAHAWUN HAUSA I

## ABUBUWAN DA SUKE CIKI

**RUKUNI NA 1**
Kashi Na 1 Me Ake Nufi Da Nahawu?
Kashi Na 2 Rukunonin Nahawun Hausa I
Kashi Na 3 Rukunonin Nahawun Hausa II
Kashi Na 4 Rukunonin Nahawun Hausa III
Kashi Na 5 Jimla A Nahawun Hausa

**RUKUNI NA 2**
Kashi Na 1 Jimla Mai Aikatau
Kashi Na 2 Jimla Maras Aikatau
Kashi Na 3 Tsarin Jimlar Hausa
Kashi Na 4 Qarfafawa
Kashi Na 5 Ganga

**RUKUNI Na 3**
Kashi Na 1 Lokutan Hausa I
Kashi Na 2 Lokutan Hausa II
Kashi Na 3 Li’irabin Jimla I
Kashi Na 4 Li’irabin Jimla II

## RUKUNI NA 1

Kashi Na 1 Me Ake Nufi Da Nahawu?

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Me Ake Nufi Da Nahawu?
3.1.1 Nahawu A Ilimin Kimiyyar Harshe
3.2 Dalilin Samuwar Nahawu A Harshe
3.3 Nahawun Hausa
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayani a kan abin da ake nufi da "Nahawu" da yadda kalmar ta samo asali da matsayinta a ilimin kimiyyar harshe da ma'anar da take xauke da ita a ilimin kimiyyar harshe da kuma dalilin samuwar "Nahawu" a harshe. Wannan kashi zai bayyana maka cewa isar da sako ta hanyar amfani da harshen xan'adam yana xauke da wani tsari da ya danganci ba kara zube yake ba. Kowace al'umma tana da harshen da take yin amfani da shi wajen sadarwa ko isar da saqo amma saqon ba ya isa yadda ya kamata sai an bi wani tsari da zai tabbatar da shi. Wannan tsari qunshe yake cikin abin da wannan kashi zai gabatar maka da shi. Wato dai babu wata al'umma da za a ce ba ta da harshen sadarwa. Harshe shi ne tubalin ginin al'umma. Nahawu kuwa ginshiqi ne wajen tabbatar da harshe a matsayin tubalin ginin al'umma da fahimtar juna da kuma kyautata zamantakewar al'umma har a samu ci-gaba. Wannan yana xaya daga cikin dalilan da suka sa ake samun kimiyyar harshe na harsunan daban-daban. Misali, kimiyyar harshen Hausa da kimiyyar harshen Larabci da kimiyyar harshen Ingilishi da kimiyyar harshen Faransanci da sauransu. Wato dai, a wannan kashi za ka kuma fahimci cewa "Nahawu" wani vangare ne na ilimin kimiyyar harshen Hausa. Wannan kashi zai

haskaka maka ka fahimci cewa ma’anar abin da aka furta ko aka rubuta ba ta cika sai an bi tsari na nahawun harshe.

## 2.0 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi ana so ka fahimci:

- Abin da ake nufi da nahawu.
- Matsayin nahawu a fagen ilimin kimiyyar harshe.
- Dalilin samuwar nahawu a harshe.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Me Ake Nufi Da Nahawu?

A nan zan gabatar maka da abin da ake nufi da nahawu, amma kafin na kai ka ga ma’anar nahawu zai fi kyau ka fara fahimtar abin da ya haifar da nahawu. Harshe shi ne ya haifar da abin da ake kira nahawu. Saboda haka yana da kyau ka fahimci cewa harshe da al’umma tamkar jini da tsoka ne. Matuqar an samu al’umma, to lallai kuwa a samu al’ummar tana da harshenta na sadarwa. Wannan na yin nuni da cewa kowace al’umma tana da nata irin harshen. Wannan shi ya haifar da samuwar harsuna masu tarin yawa a faxin duniya. Wannan dalili shi yake nuni da cewa harshen xan’adam ba kara-zube yake ba yana da tsari da hanyar nazarinsa. Daga cikin hanyoyin da aka gina harshen xan’adam a kai har a samu isar da saqo da ma’ana akwai abin da ake kira nahawu. Duk maganar da xan’adam yake furtawa ko rubutawa tana xauke da tsari na nahawu. Kalmar “Nahawu” asalinta daga harshen Larabci ne, harshen Hausa ya ara yake kuma amfani da ita tamkar tasa. To me ake nufi da nahawu a fagen ilimi? Da farko, bari ka ji bayanin da Zarruq (2005: 9) ya yi inda yake cewa “Yayin da mutum yake magana da harshensa, an lura da cewa, ire-iren tsarin jumlolin da ke fita daga bakinsa ba su da iyaka. Yawancinsu ma a wannan lokacin yake tsara su, ba tare da ya tava ji an faxe su da wannan sigar ba. Amma duk da haka za ka iske cewa, tsarin jimlar nan da ya qirqiro ya zo ‘daidai’ da na sauran jumlolin harshen gaba xaya. Har ma idan ya xan vata tsarin da gangan ko bisa kuskure, nan da nan wanda ya san harshen zai ce masa ‘ba haka ake cewa ba’. Saboda haka wannan wata ishara ce da ke gwada cewa akwai dai wani babban ‘gwadabe’ wanda ilahirin masu magana da harshe ke bi yayin da suke magana. Ma’ana harshen yana da wasu qa’idoji a kan yadda ake tsara dukkan maganganunsa, waxanda aka furta da waxanda ma ba a tava faxi ba”. To, nahawu shi ne babban gwadaben da masu magana da harshen xan’adam suke bi yayin da suke magana kuma shi ne qa’idojin da suke bi a samu cikar magana da isar da saqo.

Bugu da qari, Bello (2014: 1) ya bayyana nahawu da cewa “…. idan an zo maganar nahawu, a kowane harshe, ana nufin yadda tsarin wannan harshe yake, tun daga

yadda kalmominsa suke, da yadda suke haxuwa da juna bisa tsari don su samar da ingantattun jumloli masu ma'ana, daidai da yadda masu wannan harshe ke sarrafa shi a cikin harkokinsu na yau da kullum". Idan har yanzu ba ka fahimci ma'anar nahawu da kyau ba bari yanzu in kawo maka ma'anarsa a tsari na waqa kamar yadda Sani (2009: 2) yake cewa:

> Shi dai ginin jimla daxa vangaren nahawu,
> Da ke nufin nazarin tsari na shi jimla.
>
> Jimla a nan wato yanki na shi magana,
> Bisa zubi na musamman don fa sadarwa.
>
> Kowacce jimla ginawa ai ka san aka yi,
> Kalma iri da iri a wuri guda a haxa.
>
> A harhaxa su daxa kan qa'idar harshe,
> Shi ne muke son nunawa cikin waqa.

Idan ka karanta waxannan baitoci guda huxu za ka ga cewa mawallafin ya fito mana da ma'anar nahawu a dunqule cikin baitocin waqa. Gaba xaya dai, a nan zan iya bayyana maka ma'anar nahawu a taqaice da cewa fanni ne na ilimin kimiyyar harshe da ya danganci yadda ake harhaxa kalmomi bisa tsari na harshe a samar da jimla ko wani yanki na jimla mai xauke da ma'ana. Kenan kalmomi su ne tubalan ginin jimla a nahawu. Kalmomi ake harhaxawa a samar da jimla. Harhaxa kalmomi ba yin sa ake yi yadda mutum ya so ba, akwai qa'idojin da harshe yake bi don samar da jimla. Nazarin waxannan qa'idoji shi ne nazarin nahawu. Idan babu kalmomi to ba za a yi maganar nazarin nahawu ba. Wanda ya qware a wannan fanni shi ake kira 'masanin nahawu'. Mene ne aikinsa? Aikinsa shi ne ya iya tsamo ko fito da qa'idojin da harshe yake gina jimla da kuma samfurinsu a taqaice. Wato dai, a taqaice, ka gane cewa nahawu dai fannin ilimi ne da ya danganci ginin jimla a harshe . Ilimin nahawu zai taimake ka ka iya rubuta ko furta zance mai ma'ana a harshe. Nahawu fanni ne na ilimi mai faxin gaske. A dalilin haka akwai buqatar mu duba matsayinsa a ilimin kimiyyar harshe. Sai mu tafi zuwa sashe na gaba.

### 3.1.1 Nahawu A Ilimin Kimiyyar Harshe

Fannin ilimin da ake nazarin harshen xan'adam a kimiyyance shi ake kira ilimin kimiyyar harshe. Ilimin kimiyyar harshe fannin ilimi ne da ake nazarin harshe bisa tsari kuma bi-da-bi. Wannan shi ya sa mafi rinjayen masana ilimin kimiyyar harshe suke ganin sa a matsayin fannin kimiyya tsantsa. Shi ya sa aka bayyana ilimin kimiyyar harshe da cewa nazari ne kan harshen xan'adam a kimiyyance. A ilimin kimiyyar harshe ana bin matakai irin na ilimin kimiyya tsantsa kamar rashin nuna

son kai da tsarin bayani da gani da ido da fitar da sakamako. A dunqule dai, ilimin kimiyyar harshe yana qoqarin samar da bayanai a kan:

- Me ake nufi da harshe?
- Yaya harshe yake samar da kalmomi?
- Me ya sa harsuna suke sauyawa?
- Ta yaya ake koyon harshe?
- Da sauransu

To, mene matsayin nahawu a ilimin kimiyyar harshe? Da farko dai, Kimiyyar harshen Hausa yana da vangarori ginshiqai da kuma ravadanni. Vangarorin da suke ginshikai sun qunshi ilimin furuci da ilimin tsarin sauti da ilimin qirar kalma (wato ilimin tasrifi) da ilimin nahawu da kuma ilimin ma'ana. An kira su da sunan ginshiqai saboda dangantakarsu ta kai tsaye da ilimin kimiyyar harshe. A nan za ka ga cewa ilimin nahawu yana xaya daga cikin ginshiqan rassa na ilimin kimiyyar harshe. Wato, ina qoqarin nuna maka cewa nazarin harshe ba zai cika ba ko ba zai yiwu ba sai da ginshiqan fannonin da aka ambata. Nahawu (ginin jimla) yana xaya daga cikinsu.

A bisa tsari na ilimin kimiyyar harshe, ilimin nahawu ya kasance tsakanin ilimin qirar kalma ko tasrifi da ilimin ma'ana. Ilimin nahawu ba ya fara aiki sai an samar da kalma ko kalmomi a harshe. Idan za a samar da jimla to sai a harhaxa kalmomi na harshe a samar da ita. Shi kuwa nahawu a ilimin kimiyyar harshe tafiya yake yi kafaxa da kafaxa da ilimin ma'ana. Domin dole kalmomin da za a haxa su bayar da jimla su kasance suna xauke da wata ma'ana. Nahawu yana da matsayi babba a ilimin kimiyyar harshe, kuma idan babu nahawu sauran ginshiqan rassan ba za su yi wani tasiri ba, kuma sadarwa tsakanin mutane ba za ta yiwu ba. Masanin ilimin kimiyyar harshe shi ne wanda yake bayyana matsayin harshe a kimiyyance ta hanyar fito da tsari da dokokin da suka kevanta da harshe dangane da nahawu ko sauran ginshiqan rassan da na ambata maka a baya.

Wannan matsayi da yanayi na ilimin kimiyyar harshe shi ya haifar da ilimin kimiyyar harshe na harsuna daban-daban. Misali, kimiyyar harshen Ingilishi da kimiyyar harshen Hausa da kimiyyar harshen Larabci da sauransu. Ilimin kimiyyar harshen Hausa fanni ne na ilimi da ya danganci nazari da binciken harshen Hausa a kimiyyance. Kimiyyar harshen Hausa nazari ne a kan tsari da siffofin da harshen Hausa ya kevanta da su a kimiyyance ko a ilmance. Tunda harshen Hausa ba kara-zube yake ba yana da tsari da ya kamata a fito da shi ta hanyar nazari daki-daki (wato a kimiyyance ke nan). Kimiyyar harshen Hausa za a iya bayyana shi da cewa fanni ne na ilimi da manazarta suke qoqarin fito da wasu dokoki da suka kevanta da Hausa tun daga furuci da tsarin sauti da ginin kalma da nahawu (ginin jimla) da

kuma ma'ana. A nan ma nuna maka cewa a ilimin kimiyyar harshen a Hausa fannin nahawu yana nan riqe da matsayinsa na kasancewa ginshiqi. Wato sai dai magana tana gudana ta hanyar furuci ko rubutu. Duk manazarcin da yake nazarin dokokin da suka kevanta da harshen Hausa ta fuskar nahawu (ko ta hanyar sauran ginshiqan rassan) shi ake kira da masanin kimiyyar harshen Hausa. Ka gane cewa akwai bambanci tsakanin mai magana da harshe da kuma mai nazarin harshe. Duk wanda yake nazarin wani harshe don ya fito da dokoki da matsalolin da suke tattare da harshen shi ne masanin kimiyyar harshen; ba daidai yake da wanda kawai shi magana yake yi da harshen ba. Tunda shi dai ba zai iya warware wasu matsalolin ilimi da suka danganci nahawun harshen ba. Wannan shi ne matsayin nazarin harshe a kimiyyance musamman ta fuskar nahawu.

## 3.2 Dalilin Samuwar Nahawu A Harshe

A wannan qaramin kashi zan gabatar maka dalilan da suka haifar da ilimin nahawu a harshe. Dalilin da ya samar da ilimin nahawu shi ne cewa harshen xan'adam ba kara zube yake ba, yana da tsari. Xaya daga cikin tsarin harshe shi ne wanda ya danganci nahawu. Ta hanyar nazarin nahawu kaxai za ka fahimci yadda dokokin harshe suke wajen gina jimla. A nan yana da kyau ka gane cewa harshen xan'adam gaba xayansa an gina shi ne a kan wani tsari ko wata qa'ida. Magana da mutane suke yi da harshe tsari suke bi na harshe wajen gina jimla ko sadarwa. Fahimtar wannan tsari shi ya haifar da samuwar ilimin nahawun harshe. Misali, ka dubi waxannan kalmomin na Hausa:

- Binta
- karanta
- littafi
- ta
- xazu

Waxannan kalmomi ne guda biyar a Hausa da za a iya haxa jimla kamar haka da su: 'Binta ta karanta littafi xazu'. Idan ka duba za ka ga cewa ba kawai rubuta sun a yi kamar yadda na ga dama ba, a'a, dole sai da na bi wani tsari na yadda ake gina jimla a Hausa. Wannan tsari shi ya tabbatar da samuwar nahawu a harshe. Har ila yau, nahawu ya samu a dalilin sanin muhallin ko gurbin kowace kalma a jimla. Misalin da na ba ka 'Binta ta karanta littafi xazu' na yi amfani da kalmomi guda biyar; 'Binta' da 'ta' da 'karanta' da 'littafi' da 'xazu'. Kowace kalma a nan na ajiye ta bisa tsarin da ya kevanta da ita, wato gurbin da ya dace da ita a tsarin ginin jimlar Hausa; da zarar na jirkita tsarin to za ka ga cewa ma'anar ba za ta fita ba, kuma ba za a fahimci abin da mutum yake son faxi ba. Da zarar Bahaushe ya ji zai ce ai wannan shirme ne kai tsaye. Ga misali: 'ta littafi xazu Binta karanta'. Dalilin cewa harshe ba kara zube yake ba shi ne dalilin da ya samar da nahawu a harshe. Samuwar nahawu a harshe ta nuna cewa magana ko zance yana da tsari da qa'ida da suka danganci nahawu. Wannan ya qara nuna maka cewa kalmomi ba kawai harhaxa su

ake yi ba a samar da wata magana ba ko isar da wani saqo ba, sai an bi tsarin da ya dace da nahawun harshen. Nan gaba kaxan zan yi maka cikakken bayani kan nahawun Hausa da dokokinsa.

## 3.3 Nahawun Hausa

Nahawu kamar yadda na yi maka bayani a baya fanni ne da ya danganci yadda harshe yake gina jimla ta hanyar bin wasu dokoki. Kowane harshe yana irin nasa nahawun da dokokinsa. Nahawun Hausa ya qunshi yadda ake gina jimla a Hausa. Harshen Hausa yana da nasa dokokin da ake bi wajen qera jimla ko wani yanki na jimla. Dokokin da ake bi wajen gina jimla su ake kira 'dokokin qirar ko ginin jimla'. Ya kamata ka sani cewa mai nazarin nahawu yana gane dokokin qirar jimla a harshe ta hanyar la'akari da yadda masu magana da harshe suke harhaxa kalmomi su samar da jimloli ko yankinsu a harshe. To, haka lamarin yake dangane da nahawun Hausa da dokokinsa. Sai an samu kalmomi sannan za a yi maganar nahawun harshe. Nahawun Hausa yana da nasa tsarin dokokin na yadda yake harhaxa kalmomi ya samar da jimla. Su waxannan kalmomi an kira su da rukunai ko rukunoni a nahawu; saboda kowace kalma a matsayin rukuni take kuma tana da gurbinta a tsarin zubin jimla a harshe. Kamar kowane nahawun harshe na duniya, haka ma nahawun Hausa kowace kalma ko rukunin kalma yana da muhallinsa a tsarin jimlar Hausa. Idan aka qi bin wannan tsari ko qa'ida to lalle a samu jimla wadda take ba daidai ba ko maras ma'ana. Misali:

1 a. Abdu ya ci abinci.
  b. Binta ta sha ruwa.
  c. Abdu ya karanta littafi xazu.
  d. Wata yarinya fara ta mari Abdu.

Abin da nake so na nuna maka a nan shi ne a misalan da na zayyana (1a zuwa d) kowace kalma na ajiye ta ne a gurbinta ko muhallinta. Duk jimlolin sun zama karvavvu a nahawun Hausa. Saboda haka duk kalmomin an ajiye su a gurbinsu kuma za su kasance a wannan gurbin a kowace irin jimla, wannan shi ne dalilin da ya sa aka kira su da 'rukuni'. Idan ka sauya wa kalmomin muhalli sai a samu matsala, ko dai jimlar ta kasance ba daidai ba ko kuma ba ta da ma'ana. Misali:

2 a. *Ci yaa Abdu abinci
  b. *Sha Binta ta ruwa
  c. *Xazu littafi ya Abdu karanta
  d. *Fara wata mari ta Abdu yarinya

Duka misalan da na nuna maka sun sava da tsarin ginin jimlar Hausa kuma kalmomin ba a yi amfani da su a gurbinsu da ya ba su matsayi na rukuni ba. Nahawun Hausa a dunqule zai taimaka maka ka iya rubuta Hausa yadda ya kamata da kuma furta ko rubuta zance mai ma'ana.

Zarruq da Wasu (2010:32) sun bayyana cewa “Nahawu shi ne sanin qa’idojin harshe” sun qara da cewa “sanin qa’idojin harshe kuwa iri biyu ne; adananne da bayyananne”. Bisa bayanin waxannan masana akwai nahawu iri biyu, su ne ‘adanannen nahawu’ da kuma ‘bayyanannen nahawu’.Adanannen nahawu shi ake kira da sanin qa’idojin harshe. Shi ne wanda kowanne xan asalin harshe yake amfani da shi, kowanne Bahaushe yana amfani da santukan Hausa kuma yana kiyaye qa’idar zantukan, domin ba kasafai Bahaushe kan yi amfani da wani baqon sauti cikin maganarsa ba, saboda haka, idan Bahaushe ya ji wata kalma wadda ba ta Hausa ba, zai gane cewa bare ce, haka kuma idan ya ji wani tsarin haxa jimla zai iya gane cewa ba a jera kalmomin bisa qa’idar Hausa ba. Alal misali idan aka kawo jimloli kamar haka:

3a. Yaro ya tafi makaranta.
b. Makaranta tafi yaro.
c. Tafi makaranta yaro.
d. Yaro makaranta tafi ya.
e. Ya makaranta tafi yaro.

Da zarar Bahaushe ya karanta waxannan jimlolin kai tsaye zai gano cewa jimlar farko ita kaxai ce daidai, domin an jera kalmomin bisa tsarin jimlar Bahaushe, don haka, ita ce karvavviyar jimla, sauran kuma jimloli ne illatattu marasa ma’ana. Shi kuwa ‘bayananen nahawu’ shi ne wanda malamai masu koyar da harshe suke da shi. Shi ne yadda masana harshen Hausa suka san qa’idojin harshen bi-da-bi, kuma suke iya bayyana kowacce kalma da yadda aka samar da ita da ajinta da matsayinta a jimla.

Saboda haka, masanin bayyanannen nahawun Hausa ne yake iya tantance cewa kalma kaza ba ta haxuwa da kalma kaza a jimlar Hausa, ko kuma kalmomi kaza da kaza sukan zo a wuri kaza kafin kalma kaza ko bayan kalma kaza a tsarin jimla. Saboda haka, a taqaice bayyanannen nahawu na samuwa ne ta hanyar yiwa harshe nazarin qwaqqwafi kamar yadda masana da manazarta ke yi a makarantu tare da taimakon littattafai. Kashi na gaba zai yi maka cikakken bayani a kan rukunonin nahawun Hausa.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashin mun tattauna kan abin da ake nufi da nahawu da kuma matsayin nahawu a fannin ilimin kimiyyar harshe. Mun tattauna kan dalilin samuwar nahawu a harshe da kuma nahawun Hausa.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- nahawu kalma ce ta Larabci harshen Hausa ya are ta.
- Nahawu yana nufin yadda ake harhaxa kalmomi a harshe bisa tsari a samar da jimloli masu xauke da ma'ana.
- Duk maganar ko sadarwar da masu magana da harshen xan'adam suke yi an gina ta ne a kan tsari na nahawu.
- Ilimin nahawu kamar yadda ka karanta yana xaya daga cikin ginshiqan sassa na ilimin kimiyyar harshe. Shi kuwa ilimin kimiyyar harshe fanni ne na ilimi da ake nazarin harshen xan'adam a kimiyyance, wato bisa tsari.
- Ka kuma gane cewa ilimin nahawu da nahawun Hausa sun samu a dalilin cewa harshe ba kara zube yake ba.

## Auna Fahimta

1. An bayyana cewa harshe xan'adam ba kara zube yake ba. Tattauna.
2. Wace irin gudunmawa ilimin nahawu yake bayarwa ta fuskar furuci?
3. Mece ce dangantakar ilimin nahawu da ilimin kimiyyar harshe?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Me ka fahimta da 'adanannen nahawu' da 'bayyanannen nahawu'?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Bishiyar Li’irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

Zarruk Muhammad Rabi’u. da Wasu. Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa. Ibadan: University Press PLC, 2010.

## Kashi Na 2 Rukunonin Nahawun Hausa 1

### Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Rukunonin Nahawun Hausa 1
3.1.1 Suna
3.1.2 Wakilin Suna
3.1.3 Harxaxxen Suna
3.1.4 Amsa-Kama
3.1.5 Sifa
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayani a kan rukunonin nahawun Hausa zubi na farko. Na kasa maka rukunonin nahawun Hausa gida uku domin ka samu sauqin fahimtarsu. Aji na farko qarqashin wannan kashi zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa da suka qunshi 'suna' da 'wakilin suna'da 'harxaxxen suna' da amsa-kama' da kuma 'sifa'. Na haxa maka waxannan rukunan a wannan kashi saboda dangantakarsu da juna.  Ya kamata ka gane cewa nahawun harshe ba ya cika sai an fayyace rukunoninsa. Wannan yana nuna maka cewa kowane harshe na xan'adam yana da irin nasa rukunonin, sai dai kawai wani lokaci a iya samun kamanci dangane da yadda ake amfani da rukunan. Su waxannan rukunonin da zan gabatar maka kalmomi ne na harshe amma saboda suna aukuwa a ginin jimla, a gurbi na musamman shi ya sa suka zama rukunoni a harshe. Wato ana kiran su da dokokin nahawun harshe. To, haka lamarin yake a nahawun Hausa. Su rukunonin nahawu ba kara zube suke ba, suna da tsari na bi da bi. A kowane nahawun harshe ana fara gabatar da rukunin suna da dangoginsa. Kamar yadda na faxa maka a wannan kashi zan fara gabatar maka da rukunin suna da dangoginsa. Shi rukuni muhimmin tubali ne na ginin jimla, idan babu shi, babu jimla. Wato dai, rukunai

daban-daban ake harhaxawa su samar da jimla. Saboda haka sanin rukunonin nahawun Hausa abu ne mai matuqar amfani wajen sanin dokokin nahawun Hausa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce ta fahimtar da kai rukunonin nahawun Hausa aji na farko. Rukunonin da za ka fahimta a qarshen wannan darasi sun haxa da:

- Suna
- Wakilin suna
- Harxaxxen suna
- Amsa-kama
- Sifa

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Rukunonin Nahawun Hausa 1

A nan zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa aji na xaya. Rukunonin da za ka nazarta a wannan aji sun qunshi 'suna' da 'wakilin suna' da 'harxaxxen suna' da 'amsa-kama' da kuma 'sifa'. Kafin na fara gabatar da su xaixai-da-xaixai zan fara da bayyana ma'anar rukuni a nahawu da dalilinsa. Sani (1999: 60) ya bayyana rukunnonin nahawu da cewa "Wasu nau'o'i ne daban-daban na kalma da ke taka muhimmiyar rawa a bayanin nahawu na harshe. Waxannan kalmomi su ne kamar: suna da wakilin suna da aikatau da sifa da bayanau". Wato dai idan ka duba da kyau za ka ga cewa dangin kalmomi shi ake kira rukunin nahawu kamar yadda Sani (2009: 2) yake cewa daga baiti na 14 zuwa na 15:

> Kowacce kalma da gurbi nan cikin jimla,
> Domin haka sai mu somo shi batun 'kalma'.
>
> Akwai rukunai da dama nan cikin nahawu,
> Waxanda kalmomi ai duk sukan faxa.

Rukuni dai batu ne na kalma da take da wani gurbi na musamman a jimla. To duk kalmomin da ka ga an yi amfani da su wajen ginin jimla to kowace kalma gurbinta rukuni ne. Misali, idan na ce da kai '**Abdu ya sayi mota jiya**'. Wannan jimla ce a Hausa tana da kalmomi guda biyar na kaurara rubutunsu don ka gane cewa '**Abdu**' da '**ya**' da '**sayi**' da '**mota**' da '**jiya**' kalmomi ne daban-daban da aka yi amfani da su a gurbi na musamman. To, su waxannan kalmomi a kan kansu 'rukunoni' a nahawun Hausa. Ka qara sanin cewa rukunoni a nahawun harshe suna da yawa kuma su ne harsasan ginin jimla. Masana nahawun Hausa irin su Galadanci (1976) da Jinju (1980) da Bagari (1986) da Zarruq (2005) da Amfani (2007) Sani (2009) da Yusuf

(2011) da Bello (2014) da sauransu sun yi bayani kan rukunonin nahawun Hausa kuma kowanne da irin hanyar da ya bi wajen fito da bayanansa da yadda ya tsara gabatar da rukunonin. A nan zan bi hanyar da Sani (2009) ya bi wajen gabatar da rukunonin nahawun Hausa bi-da-bi. Yanzu kai tsaye sai mu tafi ga bayanin rukunonin Hausa aji na xaya.

### 3.1.1 Suna

'Suna' rukuni ne daga cikin rukunan nahawun Hausa, wanda a koyaushe masana nahawun Hausa shi suke fara gabatarwa saboda muhimmancinsa ga ginin jimla. Me ake nufi da 'suna' a nahawun Hausa? Kamar yadda Zarruq (2005: 13) yake cewa "laqabin kowane rukuni da bayaninsa sun ta'allaqa ne da ma'anarsa da saqon da yake cikinsa. Ta hanyar duban ma'ana da saqon da rukuni yake son isarwa za mu bayyana ma'anarsa. Dubi misalin da Zarruq (2005: 13) ya bayar dangane da rukunin 'suna' "Suna nau'in kalma ne da ke ambaton mutum, ko wuri, ko wani abu, ko tunani; walau mai rai ko maras rai, mai qirguwa ko wanda ba ya qirguwa, zahiri ko baxini da sauransu". To me ake nufi da 'suna'? Sani (1999: 60) ya bayyana ma'anar 'suna' da cewa "Shi ne sunan abu mai rai ko maras rai, wanda ake iya gani da ido wanda ba a iyawa". Idan ka fahimci wannan bayani za mu iya cewa 'mutum' da 'zaki' da 'qwaro' da 'dutse' da 'hula' da sauransu, kowanne ya shigo cikin ma'anar suna, saboda haka 'suna' ne. Daga ma'anar suna za ka fahimci cewa 'suna' dai a matsayinsa na rukuni a nahawun Hausa iri-iri ne. Akwai ire-iren suna kamar haka:

Suna Na Yanka

Suna ne da ya kevanta ga mutum ko wani wuri da zarar an faxi sunan an san mai shi. Misali: Hafsatu ko Maryam ko Ibrahim ko Kano ko Maiduguri da sauransu.

Suna Gama-Gari

Suna ne da bai kevanta ga wani ba, abubuwa masu rai da marasa rai duk sun yi tarayya a irin wannan suna. Wato dai ka fahimta cewa suna ne akasin na yanka. Ga misalan irin wannan sunan: jaki da kaza da cinnaka da ludayi da sanyi da mutum da sauransu. Misalan da na ba ka a nan sun qunshi sunan dabba da tsuntsu da qwaro da abun fai da sunan abu voyayyen da sunan haxaka. Kuma shi suna gama-gari daga kowane nau'i nuni yake yi ga duk wani abu mai irin wannan siga ko halitta.

Suna Gagara-Qirga

Nau'i ne na suna da aka bayyana shi da sunan abun da ba ya qirguwa. Shi ya sa aka kira shi da gagara-qirga. Misali: gari (na tuwo) da yashi da gishiri da makamantansu.

Suna Tattarau

Sani (1999) ya bayyana wannan sunan da cewa nau'in suna ne da ya haxa abu fiye da xaya a lokaci guda. Sani (1999) y aba da misali da cewa idan an ce 'garke' ko na awaki ake nufi ko tumaki ko shanu da sauransu, ba dabba guda ake nufi ba. Ga wasu misalan na suna tattarau: ayari da runduna da bataliya da gungu da makamantansu.

Suna Xan Aikatau

Shi ma nau'i ne na suna wanda asalinsa daga kalmar aikatau ne. Ma'ana dai 'aikatau' ne yake samar da shi. 'Aikatau' shi ma rukuni ne a nahawun Hausa wanda yake nuni da aikin da ka yi. Duk 'suna xan aikatau' lallai ka ga cewa tushensa daga 'aikatau' ne. Ga wasu misalan 'suna xan aikatau': *wanki* da shara da *karatu* da *rubutu* da sauransu. Ka ga a nan 'suna xan aikatau' *wanki* ya fito daga 'aikatau' *wanke*. Haka ma idan ka xauki *karatu* suna ne xan aikatau da ya fito daga 'aikatau' *karanta*, haka ma *shara* tushenta daga 'aikatau' *share*. Kalmar *kamawa* da *xaurewa* da *shanyawa* duk misalai ne na 'suna xan aikatau', tushensu daga kalmar 'aikatau' *xaura* da *kama* da *shanya*.

Wani muhimmin batu da nake so ka fahimta dangane da 'suna' a nahawun Hausa shi ne jinsi da adadi. Haqiqa, 'suna' a nahawun Hausa tafiya yake yi kafaxa da kafaxa da jinsi da adadi. A nan ina nufin idan abu mai rai ko maras rai yana xauke da sunan namiji zai yi amfani da jinsin namiji. Idan kuma abun yana xauke da suna na mace zai yi amfani da kalmar jinsi tamata ba jinsin namiji ba. Duba misalin da Jinju (1980: 16) ya bayar don ka qara rarrabewa:

1a. Rago ya girma (daidai ne ka ce 'rago ne')
b. Akuya ta girma (daidai ne ka ce 'akuya ce')

Saboda haka, kuskure ne ka ce: "rago ta girma ko rago ce". Haka ma kuskure ne ka ce: "akuya ya girma ko akuya ne". Ka fahimta cewa idan suna namiji ne shi jinsi sai ya dace da suna ya zama namiji. Idan kuma suna mace ne shi jinsi sai ya dace da suna ya zama mace. Sai dai jinsin jam'i koyaushe namiji ne. Misali:

2a. Raguna ne.
b. Akuyoyi ne.

Haka kuma 'suna' zai iya zuwa a abu xaya ko kuma ya zo fiye da guda xaya, wato jam'i kamar yadda na ba ka misali da 'raguna' da 'akuyoyi' a (2a - b). Yanzu kuma sai mu tafi zuwa rukuni na gaba, wato 'wakilin suna'.

### 3.1.2 Wakilin Suna

'Wakilin suna' kamar yadda sunan ya nuna nau'i ne na kalma da yake wakiltar suna a jimla ko yankinta. Ana yin amfani da 'wakilin suna' a lokacin da bai dace a yi amfani da 'suna' ba. Domin a wasu lokutan magana kan zo inda ba a buqatar ambaton 'suna' sai dai 'wakilin suna' don kyan magana ko jimla ko wani yanki na jimla. Misali, za ka iya cewa 'shi' maimakon 'Abdu' ko 'ke' maimakon 'Binta'. A nan za ka ga cewa 'wakilin suna' kamar 'suna' yana nuni da jinsi da kuma adadi ko yawa. Tunda 'wakilin suna' yana tsaywa ne a madadin 'suna' to ai daidai ne idan ya dace da kamannin 'suna'. Sani (1999) ya nuna cewa akwai ire-iren 'wakilin suna' har guda biyar. Ga su kamar haka: 'rakavau' da 'madubi' da 'zagin aikatau' da 'nunau' da 'tambayau'. Yanzu zan bayyana maka da ma'anoninsu daki-daki kamar yadda Sani (1999: 63 - 65) ya fito da su.

Rakavau: wannan nau'i na 'wakilin suna' a rakave yake, tare kuma da cin gashin kai. Wato yana iya zama shi kaxai ba tare da ya haxu da wani abu daban ba. Sai ka duba wannan jadawalin don ganin misalan 'wakilin suna rakavau':

| Jinsi | Mai Magana Na Farko | Mai Magana na Biyu | Mai Magana Na Uku |
|---|---|---|---|
| Namiji | Ni | Kai | Shi |
| Tamata | Ni | Ke | Ita |
| Jam'i | Mu | Ku | Su |

Idan ka duba misalan da kyau za ka ga cewa duk misalan suna nuni ne ga jinsi namiji ko tamata ko jam'i.

Madubi: wakilin suna 'madubi' shi kuwa Sani (1999) ya bayyana shi da cewa inuwa ce ta 'suna' ko wakilin suna 'rakavau'. Shi kamar yadda za ka gani ba ya zaman kansa; duk inda aka ambace shi an riga an ambaci sunan ko wakilin suna 'rakavau'. Misali:

| Jinsi | Mai Magana Na Farko | Mai Magana na Biyu | Mai Magana Na Uku |
|---|---|---|---|
| Namiji | Kaina | Kanka | Kansa |
| Tamata | Kaina | Kanki | Kanta |
| Jam'i | Kanmu | Kanku | Kansu |

Kamar yadda na faxa maka tunda farko shi suna 'madubi' ba ya iya dogaro da kansa sai ya haxu da 'suna' ko suna 'rakavau'. Duba waxannan misalan:

3a. Ni *kaina*
b. Shi *kansa*

c. Ita *kanta*
d. Mu *kanmu*
e. Binta *Kanta*
f. Abdu *kansa*

Zagin aikatau: kamar yadda sunansa ya nuna, shi ma nau'i ne na 'wakilin suna' wanda yake zuwa kafin ko gaban 'aikatau', wato kalmar da take nuni da aikin da aka yi a jimla. Zagin aikatau a ko'ina da zarar ya zo a magana, to kalmar 'aikatau' tana biye da shi. An kira shi nau'in wakilin suna saboda suna yake wakilta a yayin da ya zo gaban aikatau. Duba waxannan misalan:

4 a. Binta *ta* karantaa
b. Abdu *ya* karanta
c. *Su* karanta.

Kamar yadda ka gani a misali na (4a - c), kalmar aikatau ita ce 'karanta' a duk misalan, kalmar *ta* da *ya* da *su* duk zagi suke yi wa aikatau 'karanta'. Saboda haka, a nahawun Hausa duk kalmar da ta zo gaban zagin aikatau kalma ce 'aikatau'.

Nunau: nau'i ne na wakilin suna da yake nuni ga wani abu a kusa ko a nesa. Wato, akwai nunau na kusa da nunau na nesa. Nunau iri biyu ne; akwai 'dogo' da kuma 'gajere'. Kowannensu akwai na kusa da na nesa. Nunau dogo shi ne wanda zai iya zama da kansa ba tare da ya jingina da wani abu ba. Yanzu sai ka duba misalin nunau dogo a wannan jadawalin:

| **Jinsi** | **Nunau Kusa** | **Nunau Nesa** |
|---|---|---|
| Namiji | Wannan | Wancan |
| Tamata | Wannan | Waccan |
| Jam'i | Waxannan | Waxancan |

Na yi maka bayanin cewa 'nunau dogo' zai iya zama da kansa ba tare da an jingina shi da wani abu ba. A nan duk misalan nan na 'kusa' da na 'nesa' duk za su iya zama da kansu a jimla. Misali:

5 a. *Wannan* ta yi kyau.
b. *Wannan* ya yi kyau.
c. *Wancan* rigar baqa ce.
d. *Waxannan* yaran ba su iya ba.
e. *Waxannan* rigunan sun yi kyau.

A nan yana da kyau ka gane cewa 'nunau kusa' a tsari na jinsin namiji da tamata xaya ne kamar yadda ka gani a (5a-b). Haka ma lamarin yake a zubin jam'in 'nunau kusa' kamar yadda ka gani a (5d-e).

Nunau gajere kuwa kamar yadda sunansa ya nuna ba dogo ba ne, saboda haka ba ya iya zama da kansa sai ya sami wani abu da zai iya jingina shi. Yanzu sai ka duba jadawalin da ke qasa don ka ga zubinsa:

| **Jinsi** | **Nunau Kusa** | **Nunau Nesa** |
|---|---|---|
| Namiji | -*n* nan | -*n* can |
| Tamata | -*r* nan | -*r* can |
| Jam'i | -*n* nan | -*n* nan |

Za ka iya ganin zubinsa a jimla kamar haka:

| | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 6 | a. | littafi | + | -n | nan | → | littafin nan |
| | b. | riga | + | -r | nan | → | rigar nan |
| | c. | riguna | + | -n | nan | → | rigunan nan |
| | d. | gida | + | -n | can | → | gidan can |
| | e. | fara | + | -r | can | → | farar can |
| | f. | huluna | + | -n | nan | → | hulunan nan |

Idan ka duba misalan da na nuna maka na (6a - f) za ka fahimci cewa 'nunau gajere' jingina yake yi da 'suna' da kuma 'sifa'. A misali na (6e) za ka ga cewa nunau gajere ya jingina ne ga 'sifa', wato dai 'sifa' ce ta tallafe shi. Sauran misalan kuwa duk 'suna' ne yake tallafarsa.

Tambayau: wakilin suna tambayau daga jin sunansa za ka fahimci cewa ya danganci tambaya. Ma'ana duk lokacin da aka ambace shi ka tabbata tambaya aka yi. Tambayau iri biyu ne. Akwai tambayau na gaba xaya, wato wanda ya haxa da mutum da wasu abubuwa da kuma tambayau fayyatacce wanda yake fayyacewa tsakanin mace da namiji. Misali:

7 a. Wa ya zo?
b. Me ya kawo?
c. Wanne kake so?
d. Wacce kake so?
e. Su wa?
f. Me da me kake so?
g. Waxanne?

Idan ka duba waxannan misalan za ka ga na yi amfani da 'tambayau na gaba xaya' a misali na (7a - b), inda na yi amfani 'tambayau' *wa* a matsayin tambayau na mutum da *me* a matsayin tambayau na abubuwa. Haka ma idan ka duba misali na (7e - f) su ma tambayau ne na gaba xaya a tsari na jam'i. Misali na (7b - c) kuwa misalai ne na 'tambayau fayyatacce'.

### 3.1.3 Harxaxxen Suna

Harxaxxen suna rukunin nahawun Hausa ne dangin suna kamar yadda ka ji sunansa. A matsayinsa na rukuni a Nahawun Hausa da ya aqalla ya haxa kalma biyu ko sama da haka a matsayin suna amma 'harxaxxe'. Bari ka ji yadda Sani (2009: 9) ya kawo bayaninsa a waqe kamar haka:

> **Farin-ciki** kalmar **rigar-ruwa** ka haxa,
> Har **kar-ka-taka** akwai **taka-haye** ita ma.
>
> Ga **ka-fi-zabo** haxa nan xan'uwa ka sani,
> Har **ka-fi-shanu-wuya** duk misalansu.
>
> Doki fa **taka-haye** Sarki ya ba ka jiya,
> Shi **kar-ka-taka** kuwa, matarsa tai yi masa.
>
> **Farin-ciki** rannan a wajensa na da yawa,
> **Rigar-ruwa** sukutum shi ma ya ba Garba.

Idan ka duba za ka ga cewa Sani (2009) ya yi amfani da 'harxaxen suna' har guda goma daga baiti na 72 zuwa na 75. Ga su nan na kaurara maka su yadda z aka gane. Za ka ga na kaurara misalan harxaxxun sunaye da suka zo a baitukan. Kalmomin da suka qunshi 'harxaxxen suna' ba lallai su kasance suna ba. Wannan shi ya sa Galadanci (1976: 24) ya raba 'harxaxxen suna' zuwa gida uku kamar haka:

i. Harxaxxen suna daga suna
ii. Harxaxxen suna daga aikatau
iii. Harxaxxen suna daga amsa-kama

Galadanci (1976) ya nuna cewa 'harxaxxen suna' tushensa zai iya kasancewa daga suna ko daga 'aikatau' ko kuma daga 'amsa-kama'. Ga misalansu ka duba kamar yadda suka zo a littafinsa:

8 a. *tarin*-shiqa
b. *taurin*-kai
c. *farar*-wuta
d. *ruxa*-kuyangi
e. *tuma*-qasa
f. *taya*-ni-muni
g. *rub*-da-ciki
h. *fii*-da-sartse
i. *qyal*-*qyal*-banza

Idan ka duba waxannan misalan za ka ga cewa (8a-c) tushensu ‘suna’ ne, (8d-f) kuwa tushensu ‘aikatau’ ne, su kuma na (8g-i) tushensu ‘amsa-kama’ ne. Don qarin bayani sai ka duba Yusuf, (2011: 27-43).

### 3.1.4 Amsa-Kama

Bello (2014: 116) ya bayyana amsa-kama da cewa “Sunan an samo shi ne daga yadda kalmomin ke amfani ta hanyoyi iri-iri don qarfafawa ko kamanta ma’anonin wasu kalmomi. Ma’ana kowace kalma da aka yi mata laqabi da amsa-kama tana daxa fito da ma’anar kalmar da ake so a xaukaka ko a kambama”. Wato dai, ‘amsa-kama’ shi ma xaya ne daga cikin rukunan nahawun Hausa da yake qarfafa ko kambama wani abu da aka faxa. Kalmomi irin su *fil* da *rak* da *wuf* da *wulik* da *qerere* da *qarara* da *qiris* da *zololo* da *kasaqe* da *wur* da sauransu misalai ne na ‘amsa-kama’. Don qarin bayani a kan rukunin ‘amsa-kama’ sai ka duba aikin Bello, (2014: 116- 121).

### 3.1.5 Sifa

‘Sifa’ rukuni ce muhimmi a nazarin nahawun harshe. An bayyana ‘sifa’ da cewa kalma ce da take bayyana ‘suna’. Ita kalmar ‘sifa’ a duk inda ta zo a jimla tana yin bayani ne dangane da ‘suna’. Wannan bayanin da kalmar ‘sifa’ take yi wa ‘suna’ zai iya kasancewa na kyau ko muni ko inganci ko naqasa ko launi. Misali:

9. a. Binta *fara* ce.
   b. Abdu *gajere* ne.
   c. Binta *siririya* ce
   d. Abdu *kyakkyawa* ne.
   e. Abdu *mahaukaci* ne.

Duk kalmomin da na siranta su a waxannan jimloli misalai ne na ‘sifa’. Idan ka duba za ka ga bayani suke yi game da ‘suna’. Irin wannan bayani da kalmar ‘sifa’ take yi wa ‘suna’ shi ya samar da ire-iren sifa a nahawun Hausa. Akwai nau’i na ‘sifa’ da ake kira sassauqa kamar kalmar ‘sifa’ da na yi amfani da ita a misali na (9). Akwai ‘sifa nanatau’, wato wadda take da tsari na maimaici kamar *buhu-buhu* ko *kashi-kashi* ko *tsibi-tsibi* da sauransu. Akwai kuma wani ajin na ‘sifa’ da tushenta ‘aikatau’ ne, ana kiran ta da ‘sifa ‘yar aikatau’. Duba waxannan misalai:

10 a. dafaffe
dafaffiya
dafaffu

b. kamamme
kamammiya
kamammu

c. ginanne
ginanniya
ginannu

Duka waxannan misalai idan ka duba tushensu daga ‘aikatau’ ne. Kalmomin ‘aikatau’ da aka samar da misalai na (10a-c) ‘sifa ‘yar aikatau’ su ne *dafa* da *kama* da kuma *gina*. A nan ka gane cewa *kamamme* da *kamammiya* da *kamammu* duk tushensu daga kalmar aikatau *kama* ne.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan rukunonin nahawun Hausa aji na xaya. Rukunonin nahawun Hausa da muka yi nazari a wannan ajin sun qunshi ‘suna’ da ‘wakilin suna’ da ‘harxaxxen suna’ da ‘amsa-kama da kuma sifa.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Kowane harshe yana da rukunonin nahawu da suka kevanta shi.
- Kashi na farko da muka yi nazari su ne ‘suna’ da ‘wakilin suna’ da ‘harxaxxen suna’ da ‘ams-kama’ da kuma ‘sifa’.
- Wannan ajin kamar yadda na yi maka bayani suna da alaqa da juna. Domin kuwa dangogin ‘suna’ ne.
- Kuma ka fahimci yadda jinsi da adadi suke yin tasiri a waxannan rukunonin.

## Auna Fahimta

1. Yi bayanin yadda jinsi da adadi suka taka rawa a rukunin ‘suna’ da ‘wakilin suna’ da kuma ‘sifa’.
2. Rukunin ‘suna’ da na ‘wakilin suna’ tamkar wa da qani ne a nahawun Hausa. Tattauna.

## 6,0 Jingar Aiki

1. Kawo misalai goma sha biyar (15) na 'harxaxxen suna' da tushensu 'aikatau ne?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

# Kashi Na 3 Rukunonin Nahawun Hausa II

## Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Rukunonin Nahawun Hausa II
3.1.1 Aikatau
3.1.1.1 So-Karvau
3.1.1.2 Qi-Karvau
3.1.2 Bayanau
3.1.3 Sarqaqqiyar Nasaba
3.1.4 Ma'auni
3.1.5 'Yar Mallaka
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

## 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayani a kan rukunonin nahawun Hausa zubi na biyu. Na kasa maka rukunonin nahawun Hausa zuwa gida-gida domin ka samu sauqin fahimtarsu. Gabatar da su duk a lokaci guda zai iya rikitar da kai. Qarqashin wannan kashi zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa da suka qunshi 'aikatau' da 'bayanau' da 'nasaba' da 'ma'auni' da kuma 'haxi'. Na haxa maka waxannan rukunan a wannan kashi saboda dangantakarsu da juna. Ya kamata ka gane cewa nahawun harshe ba ya cika sai an fayyace rukunoninsa. Shi rukuni muhimmin tubali ne na ginin jimla, idan babu shi, babu jimla. Wannan yana nuna maka cewa kowane harshe na xan'adam yana da irin nasa rukunonin, sai dai kawai wani lokaci a iya samun kamanci dangane da yadda ake amfani da rukunan. Su waxannan rukunonin da zan gabatar maka kalmomi ne na harshe amma saboda suna aukuwa a ginin jimla, a gurbi na musamman shi ya sa suka zama rukunoni a harshen Hausa. Wato ana kiran su da dokokin nahawun harshe. Su rukunonin nahawu ba kara zube suke ba, suna da tsari na bi da bi. Wato dai, rukunai daban-daban ake harhaxawa su samar da jimla. Saboda haka sanin rukunonin nahawun Hausa abu ne mai matuqar amfani wajen sanin dokokin nahawun Hausa.

## 2.0 Manufar Darasi

Wannan darasin zai fahimtar da kai rukunonin nahawun Hausa aji na biyu. Rukunonin da za ka fahimta a qarshen wannan darasi sun haxa da:

- Aikatau
- Bayanau
- Nasaba
- Ma'auni
- Mahaxi

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Rukunonin Nahawun Hausa II

A nan zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa aji na biyu. Rukunonin da za ka nazarta a wannan aji sun qunshi 'aikatau' da 'bayanau' da 'nasaba' da 'ma'auni' da kuma 'haxi'. Yanzu kai tsaye sai mu tafi ga bayanin rukunonin Hausa aji na xaya.

### 3.1.1 Aikatau

'Aikatau' muhimmin rukuni ne daga cikin rukunan nahawun Hausa, wanda a koyaushe masana nahawun Hausa sai sun yi magana a kan sa saboda muhimmancinsa wajen ginin jimla. Baya ga muhimmancinsa a vangaren nahawu, aikatau ginshiqi ne a fannin ilimin kimiyyar harshe. Me ake nufi da 'aikatau' a nahawun Hausa? Zarruq (1990: 1) ya bayyana ma'anar 'aikatau' da cewa "Kalma ce mai nuna aikatawa ko aukuwa ko wakana. Kullum tana bin wakilin suna, dangin 'sun' da 'zaa su' da sauransu". Ya qara da cewa 'aikatau' kalma ce kevavviya, ba ruwanta da ma'anar qwadago ko aikin lada irin wanda mata sukan yi. Wannan ita ce kalmar da ake kira 'fi'ili' a wasu littattafan. Ga misali zan ba ka don ka fahimci kalmar aikatau a jimla:

1a. Abdu ya *ci* abinciSani.
b. Binta ta *tafi* makaranta.
c. Abdu da Binta za su *yi* wasa.
d. Abdu da Binta sun *yanka* nama.
e. Abdu ya *kishingixa*.
f. Mun *karanta* littafi.

Kamar yadda Zarruq (1990) ya bayyana kalmar 'aikatau' ana gane ta yayin da ta biyo zagin aikatau, kamar yadda sunansa ya nuna shi ma nau'i ne na 'wakilin suna' wanda yake zuwa kafin ko gaban 'aikatau', misali 'ya, ta, sun, mun' da sauran danginsu. Duk kalmar da ta zo bayan 'zagin aikatau' ita ake kira da suna 'aikatau',

saboda tana xauke da wani aiki ko wani abu da ya wakana a jimla. Idan ka duba misali na (1a-f) duk kalmomin da suka biyo zagin aikatau su ne misalan ‘aikatau’ a Hausa. Ka ga kalmar *ci* da *tafi* da *yi* da *yanka* da *kishingixa* da *karanta* duk misalai ne na ‘aikatau’.

### 3.1.1.1 Aikatau So-Karvau

Kamar yadda sunansa ya nuna shi irn wannan aikatau a koyaushe karvau ne yake biyo aikatau xin da ya zo a cikin jimla. Karvau shi ne sunan da ya biyo bayan aikatau. An bayyana shi da karvau saboda shi aikin ya fadawa. Wannan shi ne dalilin da ya sa ake kiran sa da ‘aikatau so-karvau’. Ga misalan ‘aikatau so[karvau kamar haka:

2a. Binta ta *dafa* shinkafa.
b. Abdu ya *mari* Binta.
c. Abdu ya *wanke* mota.
d. Sun *yanka* nama.

A nan ‘aikatau’ *dafa* da *mari* da *wanke* da *kuma yanka* duk karvau ya biyo su. Saboda haka waxannan aikatau xin da makamantansu su ake kira ‘aikatau so-karvau. Yanzu kuma zan gabatar maka da ‘aikatau qi-karvau’.

### 3.1.1.2 Aikatau Qi-Karvau

Shi kuwa ‘aikatau qi-karvau’ kamar yadda sunansa ya nuna akasi ne na ‘aikatau s0-karvau. Wato, ‘aikatau qi-karvau’ nau’i ne na aikatau da karvau ba ya biyo shi. Saboda haka aikin da ya wanzu a cikin jimla komawa yake yi ga wanda ya yi aikin, wato aikau. Ga wasu misalan jimloli masu xauke da ‘aikatau qi-karvau’ kamar yadda Sani (1999: 66) ya kawo:

3a. Abdu ya *gudu.*
b. Tulun ya *cika*.
c. Yarinyar ta *rasu.*
d. Shinkafar ta *dafu*.

Idan ka duba misalan da kyau za ka ga cewa aikin da ya zo cikin kowace jimla komawa yake yi ga wanda ya yi aikin ko wakanar aikin. Wato dai aikin (ko wakanar aikin) ana danganta shi ne ga sunan da aka fara ambatawa kamar yadda ka gani a (3a-d). Ka ga *gudu* da *cika* da *rasu* da *dafu* dukkansu misalai ne na ‘aikatau qi-karvau’.

### 3.1.2 Bayanau

Bayanau rukuni ne da yake da matuqar muhimmanci a nahawun Hausa. Rawar da bayanau yake takawa ita ce bayyana aikatau da fito da yadda aka yi wani aiki a jimla. To idan an ce 'bayanau' me ake nufi? Bayanau a nahawun Hausa kalmomi ne da suke bayyana yadda wani abu ya faru da lokacin da ya faru da kuma wurin da abin ya faru. Misali, 'bayanau' yana nuna shin abu ya faru da sauri ne ko a hankali. 'Bayanau' yana kuma rarrabe yawa ko qanqantar abu. Misali, idan ake ce 'Abdu ya rubuta wasiqa *xazu*', kalmar *xazu* a nan ita ce bayanau domin tana bayyana lokacin da aka rubuta wasiqar. Kalmomin 'bayanau' suna da yawa hakan shi ya haifar da 'bayanau' iri-iri. Yanzu zan kawo maka ire-iren bayanau kamar haka:

#### 3.1.2.1 Sassauqan Bayanau

Sassauqan bayanau nau'i ne na bayanau da ya qunshi kalmomi xai-xai da waxanda aka nanata / maimaita ko ninka wani vangare na kalma ko kuma kalmar gaba xaya da kuma waxanda suke nuna yadda wani abu ya kasance ko tsananinsa da qarfinsa. Irin wannan bayanau zai iya kasancewa haxaxxe (kamar a misali na 4a-c) ko nanatau (kamar a misali na 4d-f) ko kuma tsanantau (kamar a misali na 4g-i).

4a. xazu
b. yanzu
c. bana
d. yanzu-yanzu
e. xazu-xazu
f. yayyanke
g. ainun
h. matuqa
i. sosai

#### 3.1.2.2 Harxaxxen Bayanau

Sani (1999: 69-70) ya bayyana 'harxaxxen bayanau kamar haka:
"Harxaxxen bayanau ya qunshi kalma fiye da xaya. Ana samun 'suna' ne ko 'bayanau sassauqa' a farko, sannan 'sarqaqqiyar nasaba gajeriya' ko 'yar mallaka gajeriya' ta biyo baya". Ga misalansu:

Suna + sarqaqqiyar nasaba gajeriya
5a. bakin qofa (baki + -n)
b. gavar kogi (gava + -r)

Suna + 'yar mallaka gajeriya
c. kamarsa (kama + -rsa)
d. shigensu (shige + -nsu)

e. yanayinta (yanayi + -nta)

Sassauqan bayanau + sarqaqqiyar nasaba gajeriya

f. wajen gari (waje + -n)
g. cikin mota (ciki + -n)
h. gefen hanya (gefe + -n)

Sassauqan bayanau + ‘yar mallaka gajeriya

i. wajensa (waje + nsa)
j. cikinta (ciki + nta)
k. gefenta (gefe + -nta)

Duk misalan da na bayyana maka daga (5a-k) duk sun danganci harxaxxen bayanau. Abu biyu suna da matuqar muhimmanci na farko akwai sarqaqqiyar nasaba, wato -*n* da -*r* da suke zuwa a jikin ‘suna’ kamar a misali na (5a-b) ko ‘sassauqan bayanau’ kamar a misali na (5f-h). Zan yi maka cikakken bayani a kan ‘sarqaqqiyar nasaba’ a sashe na 3.1.3. Sai kuma ‘yar mallaka gajeriya’, wato -*nta* da -nsa da ake rava su a jikin ‘suna’ kamar a misali na (5c-e) ko ‘sassauqan bayanau’ kamar yadda na nuna maka a misali na (5i-k). ‘Yar mallaka gajeriya kamar yadda sunan ya nuna tana bayyana mallakar abu ne kamar yadda aka yi amfani da ita a misalan da na nuna.

### 3.1.3 Sarqaqqiyar Nasaba

‘Sarqaqqiyar nasaba’ harafi ne da yake nuna nasabar ko dangantakar wani abu da wani. ‘Sarqaqqiyar nasaba iri biyu ce, akwai gajeriya da kuma doguwa. Gajeriyar ta qunshi harufa kamar haka; -*n* da -*r* ; ita kuma doguwar tana da *na* da *ta*. Gajeriyar sarqaqqiyar nasaba koyaushe a jikin suna take sannan ‘suna’ ya biyo bayanta kamar a misali na (5a-b), ita kuwa doguwar sarqaqqiyar nasaba tana zuwa ne kafin suna. Wato ana danganta ta da sunan da ya zo a bayanta. Misali, mota *ta haya*, fadama *ta rake* da makamantansu.

### 3.1.4 Ma’auni

‘Ma’auni’ rukunin nahawu ne da yake nuna adadi ko yawan abu. ‘Ma’auni ya kasu gida uku. Na farko shi ne ‘ma’auni’ ta hanyar qidaya kamar a ce *xaya, biyu uku, goma, ashirin, xari, dubu* da sauransu. Na biyu shi ne ‘ma’auni’ ta hanyar amfani da kalmomi kamar *kaxan, da yawa, da dama, barkatai, tuli* da makamantansu. Ma’auni na uku shi ne wanda ya shafi yin maimaici ko ninki cikakke ko ragagge na ma’auni na qidaya ko ma’auni na wasu kalmomi. Misali:

6a. huxu-huxu
b. dubu-dubu
c. xari-xari
d. hurhuxu
e. bibbiyu

f. kaxan-kaxan

s

Idan ka duba misalan za ka ga cewa (6a-c) sun danganci cikakken ninkin ma'auni ta hanyar qidaya, amma (6d-e) sun shafi ninki ragagge na ma'auni ta hanyar qidaya, shi kuwa (6f) nuni yake yi ga maimaita ma'aunin wasu kalmomi.

### 3.1.5 'Yar Mallaka

'Yar mallaka tana da matuqar muhimmanci a nahawun Hausa. 'Yar mallaka kamar yadda sunan ya nuna tana bayyana mallakar wani abu. 'Yar mallaka iri biyu ce, akwai doguwa da kuma gajeriya. Doguwar 'yar mallaka a koyaushe ba a haxe take da abin da aka mallaka ba, wato dai zaman kanta take yi ba haxa ta ake yi da wata kalmar ba. Misalin kalmomin doguwar mallaka su ne kamar *nawa* da *naka* da *namu* da *nasu* da *tata* da *tamu* da *naku* da makamantansu. Idan na ce, 'wata mota *tawa* ta lalace'. Ka ga kalmar doguwar 'yar mallaka *tawa* ba a haxa ta da abin da aka mallaka ba, wato *mota*.
Gajeriyar 'yar mallaka kuwa ita koyaushe haxe take da abin da aka mallaka. Gajeriyar 'yar mallaka qwayar kalma ce (wato ba cikakkiyar kalma ba ce) dole sai an jingina ta a jikin wata kalmar. Misali, idan aka ce *gona**rsa*** ko *riga**rsa*** ko *gida**nmu*** ko *mota**rta*** da sauransu. A nan idan ka xauke *gona* da *riga* da *gida* da *mota* to sauran qwayoyin kalmomin su ne misalan 'yar mallaka gajeriya. Misalin gajeriyar mallaka a jimla shi ne 'mota**rmu** tana da kyau'.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan rukunonin nahawun Hausa aji na biyu. Rukunonin nahawun Hausa da muka yi nazari a wannan ajin sun qunshi 'aikatau' da 'bayanau' da 'sarqaqqiyar nasaba' da 'ma'auni' da kuma 'yar mallaka'.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- kowane harshe yana da rukunonin nahawu da suka kevanta shi.
- A wannan kashin rukunonin da muka yi nazari su ne 'aikatau' da 'bayanau' da 'sarqaqqiyar nasaba' da 'ma'auni' da kuma ''yar mallaka'.
- 'Aikatau' muhimmin rukuni ne wanda ya qunshi aiki ko wani abu da ya wanzu a tsarin zance ko jimla.

- ‘Bayanau’ kamar yadda na faxa maka rukuni ne da yake fayyace yadda aiki ya gudana a tsarin zance ko jimla.
- ‘Yar mallaka gajeriya’ koyaushe haxe take zuwa da abin da aka mallaka. ‘Sarqaqqiyar nasaba gajeriya’ita ma tana haxe ne a jikin ‘suna’.
- ‘Ma’auni’ yana kasancewa a zubi na kalma ko ninkin kalma, wato a samu nannagen kalma cikakke ko kuma ragagge.

## Auna Fahimta

1. Yi bayanin yadda ‘aikatau’ yake da alaqa da ‘bayanau’.
2. Kawo rukunan nahawun Hausa biyu da ake samun ninki ko nannage a cikinsu.

## 6.0 Jingar Aiki

1. Bayyana kamanci da bambanci tsakanin sarqaqqiyar nasaba gajeriya da ‘yar mallaka gajeriya a nahawun Hausa.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu’azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 4 Rukunonin Nahawun Hausa III

### Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Rukunonin Nahawun Hausa III
3.1.1 Dirka
3.1.2 Tsigilau
3.1.3 Madanganci
3.1.4 Mafayyaci
3.1.4.1 Tambayau
3.1.4.2 Dunqulau
3.1.4.3 Nunau
3.1.5 Mahaxi
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayani a kan rukunonin nahawun Hausa aji na uku. Na kasa maka rukunonin nahawun Hausa zuwa gida-gida domin ka samu sauqin fahimtarsu. Gabatar da su duk a lokaci guda zai iya rikitar da kai. Qarqashin wannan kashi zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa da suka qunshi ‘dirka’ da ‘tsigilau’ da ‘madanganci’ da ‘mafayyaci’ da kuma ‘mahaxi’. Ya kamata ka gane cewa nahawun harshe ba ya cika sai an fayyace rukunoninsa. Shi rukuni muhimmin tubali ne na ginin jimla, idan babu shi, babu jimla. Wannan yana nuna maka cewa kowane harshe na xan’adam yana da irin nasa rukunonin, sai dai kawai wani lokaci a iya samun kamanci dangane da yadda ake amfani da rukunan. Su waxannan rukunonin da zan gabatar maka kalmomi ne na harshe amma saboda suna aukuwa a ginin jimla, a gurbi na musamman shi ya sa suka zama rukunoni a nahawun harshen Hausa. Wato ana kiran su da dokokin nahawun harshe. Wato dai, rukunai daban-daban ake harhaxawa su samar da jimla ko yankinta. Saboda haka sanin rukunonin nahawun Hausa abu ne mai matuqar amfani wajen sanin dokokin ginin jimlar Hausa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce ya koyar da kai rukunonin nahawun Hausa aji na uku. Rukunonin da za ka fahimta a qarshen wannan darasi sun haxa da:

- Dirka
- Tsigilau
- Madanganci
- Mafayyaci
- Mahaxi

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Rukunonin Nahawun Hausa III

A nan zan gabatar maka da rukunonin nahawun Hausa aji na biyu. Rukunonin da za ka nazarta a wannan aji sun qunshi 'aikatau' da 'bayanau' da 'nasaba' da 'ma'auni' da kuma 'haxi'. Yanzu kai tsaye sai mu tafi ga bayanin rukunonin Hausa aji na uku.

### 3.1.1 Dirka

'Dirka' rukuni ce mai matuqar muhimmanci a nahawun Hausa.Me ake nufi da dirka? 'Dirka' kalmomi ne da suke jaddada ko tabbatar da kalmar da ta gaba ce ta. Kalmomin 'dirka' a Daidaitacciyar Hausa iri biyu ne. Akwai kalmar 'dirka' '**ce'** wadda take tabbatar da kalmar 'suna' ta jinsin mace**,** da kuma '**ne'** wadda take dirke ko tabbatar da kalmar'suna' ta jinsin namiji. Ana kuma qara yin amfani da '**ne'** don jaddada kalmar 'suna' ta jam'i a jinsin namiji ko mace. Misali, riga **ce** (dirka **ce** mai jaddada jinsin mace), jirgi **ne** ('dirka' **ne** mai jaddada jinsin namiji), motoci **ne** ('dirka' mai jaddada jam'i ta fuskar jinsin mace ko namiji). Haka kuma ana yin amfani da 'dirka' don tabbatar da 'sifa'. Misali, fara **ce,** kore **ne,** koriya **ce,** dogo **ne,** siriri **ne,** sirara **ne,** da makamantansu. Yanzu duba waxannan misalan don ka ga yadda ake yin amfani da 'dirka' a cikin jimla:

1a. Abdu **ne** ya *ci* abinci.
b. Binta **ce** ta *tafi* makaranta.
c. Xalibai **ne** za su *yi* wasa.
d. Wannan mota **ce**.
e. Waxannan motoci **ne**.
f. Gida **ne**.

### 3.1.2 Tsigilau

'Tsigilau' wanda wasu masana kan kira 'tsigalau' rukunin nahawu ne da yake nuni

qanqantar abu kamar yadda Sani (2009: 30) yake cewa a waxannan baitukan:

> ‘Tsigilau a nan shi ma dai rukkunin nahawu,
> Mai nuna qanqanta ke nan daxa, ka jiya.
>
> Nan xan da ‘yar har ‘yan su ne misalansa,
> Ga ma cikakken misali nan cikin jimla.
>
> An ba shi xan wando har ma da ‘yar riga,
> ‘Yan littafai da ma can duk fa ya karva.
>
> Xan dai a nan namiji, ‘yar ko daxa tamata,
> Amma ko kalmar ‘yan jam’i ta jivanta.

Idan ka yi nazarin waxannan baitoci za ka gane cewa ‘tsigilau’ dai nuni yake yi ga qanqantar abu, kuma kalmominsa su ne *xan* da *‘yar* da kuma ‘*yan*. *Xan* ana yin amfani da shi wajen nuna jinsin namiji, *‘yar* wajen nuna jinsin mace, ‘*yan* kuma wajen nuna jam’in abu jinsin namiji ko jinsin tamata. Akasari idan kalmomin tsigilau suka zo a jimla to ‘suna’ ne yake biye da su kamar yadda na nuna maka a (2a-c) ko kuma ‘sifa’ kamar a (2d-e).

2a. Wani *xan* **yaro** ya zo aji.
b. Wata ‘*yar* **yarinya** ta kama mage.
c. Wasu ‘*yan* **makaranta** sun zo.
d. Wata yarinya *‘yar* **qaram**a ta zo.
e. Wani yaro *xan* **gajere** ya sayi keke.

3.1.3 Madanganci

Madanganci rukuni ne a nahawun Hausa da yake fayyace wani abu. ‘Madanganci’ dai a Hausa iri biyu ne, akwai -*r* da -*n*. Waxannan harufa a haka yadda suke za a iya cewa ba sa xauke da wata ma’ana, amma da yake suna zuwa ne a qarshen ‘suna’ ko ‘sifa’ suna xauke da ma’anar cewa an san abin da ake yin magana a kan sa. Misali, idan aka ce:

3a. Riga**r** ta yage.
b. Wando**n** ya qone.
c. Motoci**n sun** sun tafi xazu.
d. Fara**r** ta fi kyau.

Duk misalan suna nuna maka cewa harufan ‘madanganci’ a duk inda suka zo suna nuni da cewa an san abin da ake yin magana a kan sa. Su waxannan harufa a kullum suna zuwa ne haxe da ‘suna’ (kamar a misali na 3a-c) ko ‘sifa’ (kamar a 3d). Idan

da za a cire su sai abubuwan da aka ambata su kasance ba a san su ba. Duba misali na (4a-c).

4a. Riga ta yage
b. Motoci sun tafi xazu.
c. Wando ya qone.

Idan ka duba misali na (4a-c), duk abubuwan da aka ambata ba a san su ba, amma da zarar an liqa musu harufan 'madanganci' (kamar yadda suka zo a misali na 3a-d) za su xauki ma'anar an san abubuwan da ake magana a kan su.

1.1.4 Mafayyaci

'Mafayyaci' rukuni ne da yake taka rawa wajen fayyace jinsin abin da ake magana a kan sa. Kamar yadda sunan ya nuna 'mafayyaci' fayyace abu yake yi ta fuskar jinsin abin kamar yadda zan misalta maka nan gaba kaxan. 'Mafayyaci' Kamar yadda Sani (2009: 32) ya bayyana iri uku ne kamar haka:

i tambayau
ii Dunqulau
iii. nunau

3.1.4.1 Tambayau

Tambayau nau'i ne na 'mafayyaci' da ya qunshi kalmomin tambaya *wane* ko *wace* ko *waxanne*. Misali:

5a. *Wane* yaro ya zo?
b. *Wace* jaka za ki saya?
c. *Waxanne* kaya ya kawo?

Ya kamata ka fahimci cewa 'tambayau mafayyaci' suna zuwa ne a jimla mai tsarin tambaya kuma tafiya suke yi da jinsin abin da ake magana a kan sa. Misali, *wane* yana xaukar jinsin namiji, *wace* tana xaukar jinsin tamata (mace), *waxanne* tana xaukar jam'i na jinsin namiji ko tamata. Misalin da na nuna maka daga (5a - c) sun dace da wannan bayanin.

3.1.4.2 Dunqulau

Dunqulau ya bambanta da 'tambayau' domin shi ba ya zuwa da sigar tambaya, kuma nuni yake yi da cewa ba a san abu ba. Kalmomi da suke bayyana 'mafayyaci dunqulau' su ne *wata* da *wani* da kuma *wasu.* 'Dunqulau *wata* nuni take yi da jinsin tamata kuma duk sunan da zai biyo ta a daidaitacciyar Hausa jinsin tamata ne, *wani* kuwa duk sunan da zai biyo ta lallai ya kasance jinsin namiji, sai kuma *wasu* (ko *waxansu)* suna jam'i na jinsin namiji ko tamata shi yake biyo ta. Misali:

6a. Wata yarinya ta mari Binta.
b. Wata mota ta zo.
c. Wani gida ya rushe.
d. Wani mutum ya gina gida.
e. Wasu (waxansu) xalibai sun ci jarrabawa.

Haka kuma kalmomi dunqulau za su iya zuwa a jimla ba tare da 'suna' ba. Misali, za a iya cewa 'Wata ta mari Binta' ko 'Wani ya rubuta littafi a kan lissafi' da sauransu.

3.1.4.3 Nunau

Kamar yadda sunansa ya nuna, 'nunau' nau'i ne na 'mafayyaci' da ya danganci nuna wani abu. Nunau ya kasu gida biyu; akwai 'dogo' da kuma 'gajere'. Kalmomin 'nunau dogo' su ne *wannan* da *waccan* da *waxannan* da kuma *waxancan*. Kalmomin 'nunau gajere' su ne *nan* (ana yin amfani da ita ga jam'i jinsin namiji ko mace) da *can*. Yanzu ga wasu misalnsu cikin jimla:

7a. *Wannan* yaro ya iya xinki.
b. *Waccan* yarinyar ta zo xazu.
c. *Waxannan* xalibai sun jarrabawa.
d. *Waxancan* xalibai sun faxi jarrabawa.
e. Gidan *nan* ya yi kyau.
f. Motar *nan* ta fi kyau.
g. Gdan *can* ya ginu.

3.1.5 Mahaxi

A nan 'mahaxi' kamar yadda sunan ya nuna rukuni ne da ake yin amfani da shi wajen haxa kalma da kalma ko jimla da jimla. 'Mahaxi' a nahawun Hausa ya qunshi kalmomi *da* da *sannan*. Misali:

8a. Wake da shinkafa.
b. Koko *da* qosai.
c. Akwai waxanda za a gani da waxanda za a saya.
d. Abdu ya biya kuxin kayan *sannan* an ba shi rasixi.
e. Abdu ya ci wake *da* shinkafa *sannan* ya sha ruwa.

Duk misalan za ka ga cewa sun qunshi kalmar mahaxi, a (8a-b) kai tsaye an haxa kalmomi ne ta yin amfani da kalmar haxi *da*, a (8c) kuwa yankin jimla da wani yankin jimla aka haxa. Misali na (8d) an yi amfani da kalmar haxi *sannan* wajen yin haxi a cikin jimla. Misali na (8e) yana nuna maka cewa a jimla za a iya amfani da

kalmomin haxi har biyu. Yana da kyau ka qara fahimta cewa kalmomin da suke ‘yan rukuni xaya su suka fi zuwa a tsari na haxi.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan rukunonin nahawun Hausa aji na uku. Rukunonin nahawun Hausa da muka yi nazari a wannan ajin sun qunshi ‘dirka’ da ‘tsigilau’ da ‘mafayyaci’ da ‘madanganci’ da kuma ‘mahaxi’.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Kowane harshe yana da rukunonin nahawu da suka kevanta shi.
- Wannan ajin idan ka cire ‘mahaxi’ duk rukunonin suna da alaqa da bayanin jinsi.
- ‘Dirka’ da ‘tsigilau’ da ‘madanganci’ da ‘mafayyaci’ suna taka muhimmiyar rawa wajen samun daidaito da karvuwar jimlar Hausa.
- ‘Mahaxi’ ma yana taka muhimmiyar rawa ta yadda kalmomin haxi suke taimakawa wajen gajarta jimla da kuma haxa kalmomin da suke yan rukuni xaya.

## Auna Fahimta

1. Yi bayanin yadda jinsi yake taka rawa a Zubin ‘mafayyaci’ da ‘madanganci’.
2. Bayyana kamanci da bambanci tsakanin nau’o’in ‘mafayyaci’.

## 6.0 Jingar Aiki

1. Wace irin alaqa ake samu tsakanin ‘dirka’ da ‘madanganci’?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu’azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Bishiyar Li’irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 5  Jimla A Nahawun Hausa

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Ma'anar Jimla a Nahawu
3.2 Sassan Jimla
3.2.1 Yankin Suna
3.2.2 Yankin Bayani
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
    Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayanin jimla a nahawun Hausa. Jimla tana da matukar muhimmanci a ilimin nahawu. Domin ilimin nahawu gaba xaya an xora shi a gwadaben samar da jimla. Yana da kyau na qara fahimtar da kai cewa shi nahawu reshe ne na ilimin kimiyyar harshe da ya danganci yadda ake harhaxa kalmomi don a gina jimla. Su waxannan kalmomi da ake amfani da su wajen ginin jimla su ake kira rukunonin nahawu. Kamar yadda ka nazarce su a baya, kowane harshe yana da tsarin yadda yake amfani da su don samar da jimla. To wannan kashi zai gabatar maka da ma'anar jimla da yadda sassanta suke a nahawun Hausa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da kai:

- abin da ake kira jimla da sassanta a nahawun Hausa.
- da kuma yadda ake gina ta a nahawun Hausa. Wato, sanin sassanta da rukunonin da suka qunsa.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Ma'anar Jimla a Nahawu

Jimla a ilimin nahawu magana ce da aka furta ko aka rubuta da take xauke da ma'ana. Duk maganar da aka furta ko aka rubuta bisa dokokin nahawun harshe mai xauke da ma'ana ita ake kira jimla. Bello (2014: 122) ya bayyana ma'anar jimla da cewa "kalma ce da take nufin yadda aka jera kalmomin Hausa cikin wani tsari mai ma'ana bisa qa'ida don samar da wani furuci wanda za a iya yi ko a rubuta. Tsari ke gudanar da jimla a harshe. Kuma jimlar ta dace da yadda masu wannan harshen ke sarrafa harshensu". Wannan bayani da Bello (2014) ya yi ya fito da ginshiqan abubuwan da ake nema dangane da cikar ma'anar jimla. Da farko dai, jimla lallai ta kasance an gina ta bisa wani tsari da ya kevanta ga harshe. Ya kamata ka sani cewa kowane harshen a duniya yana da nasa irin tsarin da ake bi wajen samar da jimla, kuma duk jimlar da ta sava da wannan tsari to za ta kasance ba karvavviya ba. Wato, za ta kasance mai matsala ko kuma a ce ta sava da dokokin nahawun harshe. Misali, idan aka ce a Hausa 'Abdu ta karanta littafi', wannan jimlar ba ta zama karvavviya ba saboda ta sava da qa'idar nahawun Hausa. A qa'idar nahawun Hausa dole ne zagin aikatau ya dace da jinsin sunan da aka ambata a farkon jimla. Abu na biyu dangane da siffar jimla shi ne 'ma'ana', duk abin da aka furta ko aka rubuta idan babu ma'ana a cikinsa to bai zama jimla ba. Idan na ce 'Abdu ya ci abinci', wannan zance ne cikakke mai ma'ana saboda haka ya zama jimla. Abu na uku da ya danganci zubin jimla shi ne jimla ta dace da yadda masu magana da harshe suke sarrafa harshensu. A dunqule, dai, jimla ta qunshi yadda ake harhaxa kalmomin rukunan harshe bisa tsarin da ya dace da harshe mai xauke da ma'ana ko wani saqo. Jimla kacokan an gina ta ne a kan wani tsari, to, wane irin tsari ginin jimla ya qunsa? Wannan shi ya kawo mu kan batun sassan jimla.

## 3.2 Sassan Jimla

Tunda ka fahimci cewa 'jimla' magana ce cikakkiya mai ma'ana da aka gina a kan dokokin harshe, kuma kalmomi (wato rukunan) su tubalan ginin jimla. Misali:

| 'Abdu | ya | mari | wani | yaro | xazu' |
|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 |

A nan an yi amfani da kalmomi guda shida wajen gina wannan jimlar. Adadin kalmomin ginin jimla ya danganta da saqon da jimlar za ta isar. Wata jimlar kan iya

xaukar kalmomi sama da goma ko qasa da haka. Tunda ka fahimci cewa kalmomi su ne tubalan ginin jimla, yanzu kuma zan yi maka bayanin tsarin jimlar Hausa. Wato zan kawo maka bayanin sassan jimlar Hausa. Kamar yadda Galadanci (1976) da Sani (1999) suka bayyana jimlar Hausa ta qunshi muhimman sassa guda biyu, su ne *yankin suna* da *yankin aiki* ko *yankin bayani*.

Jimla

Yankin Suna — Yankin Bayani / Aiki

3.2.1 Yankin Suna

Yankin suna (na taqaita shi da YSn) dai a nahawun Hausa ya qunshi bayani a kan wanda ya yi aiki (wanda ake kira da ‘aikau’). Yankin suna shi ne yake fara zuwa sannan yankin bayani ya biyo shi. A sashen yankin suna ana bayyana sunan wanda ya yi aiki, wato ‘aikau’ ban da kalmar da ta danganci aikin da aka yi a jimlar. Misali:

1. Abdu ya ci abinci.

   YSn

A wannan misalin ‘Abdu’ a mtsayin rukunin ‘suna’ shi ya zo qarqashin YSn. Amma ya kamata ka sani cewa ba sunan yanka ne kawai yake zuwa a YSn ba, sauran rukunan nahawun Hausa dangin ‘suna’ za su iya kasance a YSn kamar yadda za ka gani a misalai masu zuwa:

2. Waxannan sun fi kyau.

   YSn

3. Ta tafi makaranta.

   YSn

4. Mota ta zo yanzu.

   YSn

Idan ka duba misali na (2-4) duk an yi amfani da dangin ‘suna’ a mtsayin YSn. A misali na (2) an yi amfani da ‘nunau dogo’ a matsayin YSn, a misali na (3) an yi amfani da ‘wakilin suna’ ko ‘zagin aikatau’ a YSn, a misali na (4) kuma an yi amfani da ‘suna gama-gari’. A tsari na YSn, akwai wasu kalmomin da za su iya zuwa kafin suna ko kuma bayan suna duk a qarqashin YSn. Daga cikin rukunan nahawu da za su iya zuwa kafin ‘suna’ a YSn akwai ‘sifa’ da ‘nunau’ da ‘mafayyaci’ da ‘tsigilau’ da ‘yar mallaka doguwa da sauransu.

5. Waxannan ragunan sun fi girma.  (Waxannan ‘nunau’)

   YSn

6. Wata yarinya ta tafi makaranta.  (Wata ‘mafayyaciya’)

   YSn

7. Farar riga ya saya wa Abdu. (Fara ‘sifa’)

   YSn

8. Xan doki ya ba wa Abdu. (Xan ‘tsigilau’)

   YSn

9. Tawa motar ya hau. (Tawa ‘yar mallaka doguwa’)

   YSn

Rukunan nahawu da suke biyo ‘suna’ a YSn akwai ‘sifa’ da ‘ma’auni’ da ‘madanganci’ da ‘nunau gajere’ da ‘yar mallaka gajeriya’ da sauransu. Misali:

10. Wani yaro gajere ya tafi kasuwa. (Gajere ‘sifa’)
11. Takardu kaxan ya kawo makaranta. (Kaxan ‘ma’auni’)
12. Dabbobin sun gudu. (-n ‘madanganci’)
13. Gidansa ya fi namu tsayi. (-nsa ‘yar mallaka gajeriya’)

A wannan yanki na suna duk kalmar da ta zo ana danganta ta ne da ‘suna’, wato ‘aikau’, kuma ka fahimci cewa wasu rukunonin za su iya zuwa kafin ‘aikau’ xin ko kuma bayansa.

Yankin suna yana iya qunsar wani muhimmi rukuni xaya ko biyu ko uku. Wannan Rukuni shi ake kira da siffatau (Sftn), guda uku ne amma ba lallai ne ya qunshi duka a lokaci guda ba, duk da cewa wani lokacin yakan qunshi duka wani lokaci guda xaya wani lokaci guda biyu, su ne kamar haka: siffatan goshi (za mu iya taqaita shi da Sft1) da 'siffatan ciki' (shi ne Sft2, an fi saninsa da Kai2) da kuma 'siffatan qeya' (shi ne Sft3). Sft1 su ne kalmomin da ke zuwa kafin suna, waxannan kalmomi sun haxa da: mafayyaci da tambayau da nunau da sifa da tsigalau da sauransu. Sft$^{2}$ ko K$^{2}$ wannan shi ne suna ko ma'aikaci a cikin jimla, wannan ya haxa da sunan yanka da suna gama-gari da harxaxxen suna da duk wani suna da kuma wakilin suna ma'aikaci. Shi kuwa Sft$^{3}$ kalmomi ne da suke zuwa bayan suna, sun haxa da madanganci da sarqaqqiyar nasaba gajeriya da dirka da 'yar mallaka gajeriya da makamantansu.

Bisa qa'idar jimlar Hausa wajibi ne a sami siffatan ciki (Sft$^{2}$) wanda aka fi sani da kai (K$^{2}$), amma Sft$^{1}$ da Sft$^{3}$ bayyanarsu a jimla ya danganta ne da irin tsarin jimla. Ma'ana za su iya fitowa a jimla, za kuma su iya qin fitowa. Haka kuma Sft$^{1}$ da Sft$^{3}$ za su iya qunsar kalma ko kalmomi.

Misali, yankin suna mai xauke da siffatan goshi da siffatan ciki kawai.

1.




Jimla mai xauke da siffatan ciki da siffatan qeya kawai.

15




Yankin suna mai xauke da Sft[1] da K[2] da Sft[3] ga shi a misali na (16).

16.




Yankin suna mai xauke da siffatan goshi da siffatan qeya fiye da xaya.




Yanzu kuma sai mu shiga ‘yankin bayani’.

### 3.2.2 Yankin Bayani /Aiki

Yankin bayani (na taqaita shi da YB), yanki ne mai matuqar muhimmanci a bayanin cikar jimla. YB shi ne sashen da yake yin bayani a kan YSn kuma shi ne yake xauke da aikin da ya wanzu a cikin jimla. Wato dai YB rukuni ne wajen cikar ma’ana ko isar da saqo. Misali:

14a. Abdu ya karanta littafi.

b. Binta mai hankali ce.

Jimlolin da na misalta maka a (14a da b) duk suna xauke da sassa biyu na jimla, wato YSn da YB. A misali na (14a) *Abdu* shi ne a matsayin YSn, *ya karanta littafi* kuma a matsayin YB, a (14b) kuwa *Binta* ce a YSn, *mai hankali ce* a YB. Idan ka yi nazarin waxannan jimloli za ka ga cewa a jimla ta (14a) akwai aiki, aikin shi ne *karanta littafi*. Amma jimla ta (14b) babu wani aiki da ya gudana a cikin ta. Wannan ya nuna maka cewa YB iri biyu ne, akwai YB mai xauke da ‘aikatau’ (wato YBA) da YB maras xauke da ‘aikatau’ (wato YBMA).



Yanzu bari mu kalli zubi da tsarin kowanne. YB mai aikatau, wato YBA kamar yadda sunansa ya nuna koyaushe yana xauke da ‘aikatau’. ‘Aikatau’ shi ne ginshiqi wajen fahimtar wannan yanki. Idan ka sake duba misali na (14a) za ka ga cewa ‘aikatau’ *karanta* shi ne tubali mafi muhimmanci da zarar ka xauke shi sai ka ga yankin bai xauki wata ma’ana ba. A wannan yankin ma akwai rukunan nahawu da suke zuwa kafin ‘aikatau’ da kuma bayan ‘aikatau’. Rukunonin nahawun Hausa da suke iya zuwa kafin ‘aikatau’ su ne: ‘zagin aikatau’ da ‘manunin lokaci’ da kuma qarfafau (ka duba Sani, 1999: 84). Ga wasu misalai da za su nuna hakan:

15a. Abdu **ya** zo.

b. **Ta** zo.

c. Abdu da Bala **sun** karanta.

16a. Ya*kan* zo

b. Su*kan* zo

c. Mu*kan* zo.

17a Ya *fa* zo.

b. Sun *dai* zo.

c. Ta *ma* zo.

A misali na (15a-c) na nuna maka yadda ‘zagin aikatau’ yake zuwa kafin ‘aikatau’. A nahawun Hausa duk ‘aikatau’ da ya zo a YB lallai ‘zagin aikatau’ ya gabace shi. Haka ma idan ka duba misali misali na (16 - 17). ‘Manunin lokaci’ haxe yake zuwa da ‘zagin aikatau’ idan na ce ‘ya**a** zo’, **-a** ita ce ‘manunin lokaci’, a misali na (16a-c) *kan* shi ne ‘manunin lokaci’. Zan yi maka cikakken bayani kan manunin lokaci idan na zo yi maka bayanin lokutan Hausa. Misali na (17a-c) ya qunshi misalai ne inda kalmomin qarfafawa suke zuwa kafin ‘aikatau’. Kalmomi qarfafau su ne *fa* da *dai* da *ma* da makamantansu. Yanzu kuma zan gabatar maka da abubuwan da suke zuwa bayan ‘aikatau’.

Rukunonin nahawu da suke zuwa bayan ‘aikatau’ su ne ‘suna’ da ‘wakilin suna’ da ‘sifa’ da ‘bayanau’ da kuma ‘harxaxxen suna’. Misali:

18a. Abdu ya sayi <u>mota</u>.

b. Sun tafi <u>makaranta</u>.

c. Ya kama <u>kifi</u>.

19a Abdu ya saye <u>ta.</u>

b. Ta qona kanta.

c. Mun sayi waxannan.

20a. Binta ta sayi kakkaura.

b. Mun sayi qanana.

c. Ta sayi dafaffu.

21a. Abdu ya zo yanzu.

b. Ta shigo a hankali.

c. Sun zo da sassafe.

22a. Binta ta yi farin-ciki.

b. Abdu ya sayi havar-kada.

c. Ya yi rub-da-ciki.

Tun daga misali na (18) har zuwa na (22) duk misalai ne na rukunan nahawu da suke zuwa bayan ‘aikatau’. Ka ga a misali na (18a-c) na nuna yadda ‘suna’ yake biyo ‘aikatau’ a YB. Misali na (19a-c) ‘wakilin suna’ ne suka biyo ‘aikatau’. A (20a-c) duk kalmomin da na ja layi a qasansu misalai ne na ‘sifa’ da suke iya zuwa bayan aikatau a YB. A misali na (21a-c) na nuna maka yadda ire-iren ‘bayanau’ suke biyo ‘aikatau, a na (22a-c) kuwa duk misalai ne ‘harxaxxen suna’ da suke zuwa bayan ‘aikatau’.

Yanzu kuma duba waxannan don qarin bayani:

Yanki aiki/bayani da ya qunshi gundarin aiki kaxai.

23.




Yankin aiki/bayani da ya qunshi gundarin aiki da yankin suna na biyu.

24.




A nan kuma duba yankin bayani mai xauke da aikatau da yankin suna a jimla xaya:

25.




Tunda ka fahimci YB mai aikatau, yanzu kuma sai mu juya kan YB maras aikatau.

Zubi da tsarin YB maras aikatau ya bambanta da na YB mai aikatau. Shi YB maras aikatau ya qunshi jimla wadda ba ta zuwa da aikatau, wannan shi ya haifar da cewa wasu kevavvun rukunan nahawu ne suke zuwa a nau'in YB maras aikatau. Waxannan rukunan su ne 'dirka' da 'cikamako' ko YS da 'lokaci na yanzu na xaya' da kuma 'lokaci na yanzu na biyu'. Ga wasu misalan don ka qara ganewa:

26a. Abdu ne. (misali da 'dirka')

b. Binta ce.

c. Yara ne.

27a. Binta siririyar yarinya ce. (misali da 'cikamako' + 'dirka')

b. Abdu mai hankali ne.

28a. Abdu yana wanki. (lokaci na yanzu na xaya)

b. Binta tana girki.

c. Abdu yake wanki. (lokaci na yanzu na biyu)

Waxannan (26-28) duk misalai ne na YB maras aikatau. Misali na (26a-c) 'dirka' ita kaxai ce a matsayin YB. Idan ka duba misali na (27a-b) an yi amfani da 'cikamako' ko YSn (na biyu da yake zuwa qarqashin YB) *siririyar yarinya* da *mai hankali* da kuma 'dirka'. Misali na (28a-b) suna nuna maka yadda lokaci na yanzu na xaya yake zuwa a matsayin YB. Misali na (28c) kuwa shi ya qunshi lokaci na yanzu ne na biyu).

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan jimla a nahawun Hausa. Na kawo maka ma'anar jimla a ilimin nahawu da kuma bayanin sassan jimla. Wato yankin suna (YSn) da kuma yankin bayani (YB). YB ya kasu gida biyu akwai YB mai aikatau da kuma YB maras aikatau.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Jimla a nahawun magana ce mai tsari na musamman xauke da cikakkiyar ma'ana.
- Kalmomin da suke a harshe su ne tubalan da ake yin amfani da su wajen gina jimla a harshe.
- Kalmomin da ake harhaxawa su samar da jimla su ake kira da rukunonin nahawu.
- A tsari na nahawun Hausa jimla ta qunshi yanki guda biyu, yankin suna (YSn) da kuma yankin bayani (YB).
- YSn shi yanki ne da ya kevanta da 'suna' da dangoginsa kamar 'wakilin suna' da 'sifa' da 'tsigalau' da 'yar mallaka' da 'nunau' da 'ma'auni' da makamantansu.
- YB yanki ne da yake bayyana suna, saboda haka yanki ne da ya qunshi jimla mai aikatau da maras aikatau.
- YB mai aikatau dole ne ya kasance da 'zagin aikatau' a Hausa, idan babu shi to jimlar ba za ta kasance karvavviya ba.

## Auna Fahimta

1. Wane irin tsarin jimla ne ya kevanta ga Hausa?
2. Tare da misalai bayyana rukunan nahawu da suka kevanta ga YSn.

## 6.0 Jingar Aiki

1. Kawo bayanin abin da dole sai ya zo a tsarin YB.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1977.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

**RUKUNI NA 2**

## Kashi Na 1 Jimla Mai Aikatau

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Nau'in Jimla Mai Aikatau
3.1.1 Miqaqqiya
3.1.2 Korarriya
3.1.3 Qarfafau
3.1.4 Tambayau
3.1.5 Umurtau
3.1.6 Haxaxxiya
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayanin nau'in jimla mai aikatau a nahawun Hausa. Jimla tana da matukar muhimmanci a ilimin nahawu. Domin ilimin nahawu gaba xaya an xora shi a gwadaben samar da jimla. Nau'o'in jimloli masu aikatau an gabatar da su ne ta hanyar la'akari da 'aikatau' da kuma wasu rukunonin nahawu ka yi nazari a baya. Yana da kyau na qara fahimtar da kai cewa mafi rinjayen jimlolin Hausa masu xauke da aikatau ne (duba Zarruq, 1990: 29). Saboda haka sanin ire-iren jimlolin Hausa yana da matuqar amfani. Bugu da qari, sanin rukunonin nahawu ba shi ne sanin ilimin nahawu gaba xaya ba, wani vangare ne na ilimin nahawu. Dole sai ka san yadda tsarin waxannan rukunan yake wajen samar da karvavvun jimloli. Yadda muke yin amfani da hanyoyi daban-daban wajen furta magana shi ya haifar da samuwar jimloli iri-iri masu xauke da 'aikatau' a nahawun Hausa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a qarshen darasin ka fahimci:

- nau’in jimloli masu xauke da aikatau a tsarin nahawun Hausa.
- Jimlolin Hausa sun bambanta saboda yanayin yadda muke furta kalmomi yana da yawa.
- Rukunonin nahawun Hausa suna shiga vangarori daban-daban na ginin jimlar Hausa.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Nau’in Jimla Mai Aikatau

Jimla a ilimin nahawu magana ce da aka furta ko aka rubuta bisa tsari da take xauke da ma’ana ko saqo. Duk maganar da aka furta ko aka rubuta bisa dokokin nahawun harshe mai xauke da ma’ana ita ake kira jimla. Bello (2014: 122) ya bayyana ma’anar jimla da cewa “kalma ce da take nufin yadda aka jera kalmomin Hausa cikin wani tsari mai ma’ana bisa qa’ida don samar da wani furuci wanda za a iya yi ko a rubuta. Tsari ke gudanar da jimla a harshe. Kuma jimlar ta dace da yadda masu wannan harshen ke sarrafa harshensu”. Wannan yana qara fito da cewa jimla qunshe take da wani aiki wanda wannan aikin shi ake kira da ‘aikatau’. Kamar yadda na yi maka bayani a can baya cewa tsarin jimlar Hausa akwai masu xauke da aikatau, to, yanzu a nan su za mu yi nazari don rarrabe da su. Bello (2014: 128-143) ya nuna cewa jimloli masu aikatau a Hausa sun qunshi miqaqqiya da korarriya da qarfafau da tambayau da umurtau. Yanzu zan kawo maka bayaninsu daki-daki.

### 3.1.2 Miqaqqiya

Jimla miqaqqiya ita ce wadda wasu masana nahawun Hausa suke kira da sassuqar jimla. Ita jimla ce da ka gina ta kai tsaye ba tare da wata sarqaqiya ba. Jimla da ake kira miqaqqiya ita ce kamar haka:

1a. Abdu ya karanta littafi.

b. Abdu ya doki Binta.

c. Binta ta mari Bala.

Ire-iren waxannan jimloli su ake kira da suna *miqaqqu* ko *sauqaqa*. Da farko dai suna da sauqin fahimta. Wato ba su wata rikitarwa kuma suna xauke da vangarori huxu ne kawai, su ne ‘aikau’ da ‘zagin aikatau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau’. Jimla ce mai xauke da wanda ya yi aiki, wato ‘aikau’ da ‘aikatau’ ko ‘fi’ili da kuma ‘karvau’ (wato wanda aikin ya faxawa). A nan yankin suna (YSn) shi ne yake xauke da ‘aikau’ Abdu a (1a-b) da Binta a (1c). Yankin bayani (YB) shi ne yake xauke da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau’. Akasarin jimloli an gina su a kan wannan tsarin.

### 3.1.2 Korarriya

Jimla korarriya jimla ce da take xauke da kalmar korewa a cikinta. A Hausa akwai kalmomin korewa kamar haka, *ba* da *kar* / *kada* da *babu*. Yin amfani da xaya daga cikin waxannan a jimla zai haifar da jimlar ta kasance korarriya. Misali:

2a. Binta ta dafa abinci.

b. Binta *ba* ta dafa abinci *ba*. (jimla korarriya)

A nan jimla ta (2a) sassauqa ce amma jimla ta (2b) korarriya ce saboda ta qunshi kalmomin korewa, wato *ba*. Wani misalin shi ne kamar haka:

3a. Abdu yake shuka.

b. *Ba* Abdu yake shuka *ba*. (jimla korarriya)

### 3.1.3 Qarfafau

Jimla qarfafau tana qarfafa wani abu da ya faru a jimla. Misali:

4a. Abdu ya mari Binta.

b. *Binta* Abdu ya mara. (jimla qarfafau)

A misali na (4a) babu qarfafawa a jimlar, amma idan ka duba (4b) za ka ga cewa an qarfafa cewa *Binta* fa Abdu ya mara. Wato aikin mari kanta ya faxa saboda haka ita ce 'karvau'. Zuwan 'karvau' farkon jimlar shi yake nuna qarfafawa. Wannan siga ta qarfafawa ita ta haifar da jimlar da qarfafau. Irin wannan jimlar za ta iya xaukar kalmomin qarfafawa kamar *fa, dai, kam* da sauransu. Misali:

5. *Binta fa* Abdu ya mara.

### 3.1.4 Tambayau

Jimla tambayau an kira ta da wannan suna saboda alamar tambaya da jimlar take xauke da ita. Misali:

6a. Abdu ya mari Binta.

b. Abdu ya mari Binta? (jimla tambayau)

Misali na (6b) shi ne jimla tambayau saboda alamar tambaya (?) ta zo a qarshen jimlar. Ma'ana dai za ka gane jimlar tambaya dangane da yadda aka faxe ta ko aka rubuta ta. Don qarin bayani sai ka duba (Bello, 2014: 130).

Baya ga wannan jimla tambayau za ta iya zuwa da kalmomin tambaya kamar yadda za ka gani a waxannan misalan:

7a. *Wa* Binta take so?
b. *Wa* Abdu zai aura?
c. *Wane* ya zo?
d. *Wace* mota yake so?
e. *Yaushe* jirgin zai zo?

Kalmomin tambaya kamar yadda ka gani a misali na (7a-e), kalmomi ne na musamman da suke zuwa koyaushe a farkon jimla. Wannan shi ya sa ake kiran ta jimla tambayau. A nan 'wa' da 'wane' da 'wace' da 'yaushe' duk kalmomi tambayau ne da a nahawun Hausa ake kiran su da 'wakilin suna tambayau'.

### 3.1.5 Umurtau

Jimla umurtau nuni take yi da umurni. Wato tana umartar mutum da ya yi wani aikata wani abu. Misali:

7a. Abdu, ka zo.
b. Ki karanta littafin.
c. Mu tafi yanzu.
d. Rubuta.

Duk waxannan misalai ne na jimla umurtau. Domin 'aikatau' xin duk umarni suke bayarwa. Jimla umurtau za ta iya zuwa da kalmar aikatau ita kaxai kamar a misali na (7d). Misali na (7b-c) duk sun fara ne da 'wakilin suna'. A taqaice dai, jimla umurtau za ta iya farawa da 'suna' ko 'wakilin suna' ko kuma 'aikatau'. Muhimmin abu dai dole jimlar ta zo da 'aikatau'. Wani lokaci jimlar tana iya zuwa da 'suna' da 'wakilin suna ko zagin aikatau' da kuma 'aikatau' mai sigar umarni kamar yadda na misalta maka a (7a). Kuma ka gane cewa 'aikatau' mai sigar umarni na yin wani abu a bayansa za a iya samun 'suna' (kamar a 7b, *littafi*), ko 'bayanau' (kamar a 7c, *yanzu),* haka ma wakilin suna zai iya zuwa bayan aikatau kamar ka ce 'Rubuta *ta*', a nan *ta* ita ce a matsayin 'wakilin suna' idan ka ga dama za ka iya cewa 'rubuta wasiqa'.

### 3.1.6 Harxaxxiya

Wannan jimla ce da ta qunshi jimloli fiye da xaya masu zaman kansu sai a haxe a matsayin jimla xaya ta hanyar yin amfani da 'mahaxi'. Irin wannan jimla kan zo da mahaxi da ya haxa da *kuma, sai, da, sannan* da sauransu. Misali:

8 a. Malam ya zo *amma* ya koma
b. Abdu ya sha koko *kuma* ya ci qosai

A nan, a misali na (8a), jimlar ta zo da 'suna' xaya da 'aikatau' biyu, *zo* da *koma*, an yi amfani da mahaxi *amma*. Haka ma lamarin yake a (8b), sai dai kuma an yi amfani da 'mahaxi' *kuma*.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan nau'in jimla mai aikatau a nahawun Hausa. Na bayyana maka nau'o'in jimla mai aikatau kamar haka miqaqqiya da korarriya da tambayau da qarfafau da kuma umurtau.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- jimla a nahawun magana ce mai tsari na musamman xauke da cikakkiyar ma'ana.
- Kalmomin da suke a harshe su ne tubalan da ake yin amfani da su wajen gina ta.
- Kalmomin da ake harhaxawa su samar da jimla su ake kira da rukunonin nahawu.
- A Hausa akwai jimla miqaqqiya da korarriya da qarfafau da tambayau da kuma umurtau.
- Jimla miqaqqiya ita ce jimla mai sauqi. Irin wannan jimlar tana xauke da 'aikau da zagin aikatau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'.
- Jimla korarriya kuwa dole ta xauki kalmar korewa. Idan babu kalmar korewa, jimlar komawa take zuwa miqaqqiya.
- Jimla qarfafau kuwa 'karvau' ne yake dawowa farkon jimlar don a nuna qarfafawa. Irin wannan jimlar za ta iya xaukar kalmomin jaddadawa ko qarfafawa.
- Jimla umurtau kuwa tana iya zuwa da yankin suna ko kuma ta zo da yankin bayani kawai ('wakilin suna' da 'aikatau ko kuma ma 'aikatau' shi kaxai).
- Jimla tambayau tana iya zuwa da siga biyu ko dai a yi amfani da alamar tambaya ko kuma kalmomin tambaya.
- Hausa tana da hanyoyi da dama ake yin amfani da su wajen gina jimla tambayau.

Auna Fahimta

1. Ta wace hanya za ka bambance jimla mikakkiya da jimla tambayau?
2. Shin kalmar ‘aikatau’ ita kaxai za ta iya kasancewa jimla a Hausa? Tattauna.

## 6.0 Jingar Aiki

1. Wacce irin rawa ‘bayanau’ zai iya takawa a ire-iren jimlolin Hausa?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari

Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu’azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Bishiyar Li’irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 2 Jimla Maras Aikatau

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Nau'in Jimla Maras Aikatau
3.1.1 Dirkau
3.1.2 Tambayau
3.1.3 Nunau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayanin nau'in jimlar Hausa wadda ba ta da aikatau a zubinta. Jimla tana da matukar muhimmanci a ilimin nahawu. Domin ilimin nahawu gaba xaya an xora shi a gwadaben samar da jimla. Nau'o'in jimloli marasa aikatau an gabatar da su ne ta hanyar la'akari da wasu rukunonin nahawu da ka yi nazari a baya. Yana da kyau na qara fahimtar da kai cewa akwai jimlolin Hausa masu tarin yawa da babu aikatau cikinsu. Saboda haka sanin ire-iren jimlolin Hausa marasa aikatau yana da matuqar amfani. Bugu da qari, sanin rukunonin nahawu ba shi ne sanin ilimin nahawu gaba xaya ba, wani vangare ne na ilimin nahawu. Dole sai ka san yadda tsarin waxannan rukunan yake wajen samar da karvavvun jimloli marasa aikatau. Yadda muke yin amfani da hanyoyi daban-daban wajen furta magana shi ya haifar da samuwar nau'in jimla wadda ba ta da aikatau a nahawun Hausa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da kai:

- nau'in jimloli waxanda babu aikatau a tsarinsu. J
- Ire-iren jimlolin Hausa da aka gina ba tare da yin wani aiki a cikinsu ba.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Nau'in Jimla Maras Aikatau

Jimla a ilimin nahawu magana ce da aka furta ko aka rubuta bisa tsari da take xauke da ma'ana ko saqo. Duk maganar da aka furta ko aka rubuta bisa dokokin nahawun harshe mai xauke da ma'ana ita ake kira jimla. Bello (2014: 122) ya bayyana ma'anar jimla da cewa "kalma ce da take nufin yadda aka jera kalmomin Hausa cikin wani tsari mai ma'ana bisa qa'ida don samar da wani furuci wanda za a iya yi ko a rubuta. Tsari shi ne ginshiqi wajen gudanar da jimla a harshe. Kuma jimlar ta dace da yadda masu wannan harshen ke sarrafa harshensu". Wannan yana qara fito da cewa jimla qunshe take da wani aiki ko akasinsa. Wannan shi yake qara tabbatar maka da cewa akwai jimloli marasa aikatau a harshe.

Idan aka ce jimla maras aikatau ana nufin cewa wannan magana cikakkiya ce bisa tsarin da ya dace da nahawun Hausa kuma babu wani aiki da aka yi a cikinta. Maganganu da mai magana da harshe yake yi suna zuwa ne da sigogi daban-daban. Waxanda suke zuwa da sigar da babu wani aiki a ciki su ake kira jimloli marasa aikatau. Misali, idan na ce da kai ' Abdu dogo ne', zance cikakke da aka yi da tsari kuma yake da ma'ana. Saboda haka za a iya kiran 'Abdu dogo ne' da jimla maras aikatau a nahawun Hausa. To, yanzu a nan su za mu yi nazari don rarrabe maka ire-iren jimloli marasa aikatau a nahawun Hausa. Jimloli marasa aikatau a Hausa sun qunshi 'dirkau' da kuma 'tambayau'. Yanzu zan kawo maka bayaninsu daki-daki.

### 3.1.1 Dirkau

Jimla dirkau, jimla ce da ta qunshi 'dirka' a matsayin ginshiqin tubulin gina ta. Shi ya sa ake kiran jimlar da suna 'jimla dirkau'. A tsarin irin waxannan jimloli idan aka cire 'dirka' to jimlar za ta kasance babu wata cikakkiyar ma'ana, wato ba za ta zama karvavviya a Hausa ba. Misali, idan aka ce maka 'wannan gida ne', ai jimla ce saboda cikar ma'ana da tsari. Amma idan aka cire 'dirka' ne, sai a samu 'wannan gida', ka ga babu tsari kuma ma'ana ba ta cika ba. Saboda haka a zubin irin waxannan jimloli 'dirka' rukunin nahawu ne mai matuqar muhimmmanci. 'Dirka' a nahawun Hausa su ne kalmomi kamar *ne* (ana yin amfani da ita wajen tabbatar da wani abu ko suna jinsin namiji ko kuma jam'i na jinsin namiji ko mace) da *ce* (ana yin amfani da ita wajen tabbatar da suna jinsin mace kawai). Ga misalan jimla dirkau kamar haka: kira miqaqqiya ita ce kamar haka:

1a. Abdu sarki ne.
b. Binta malama ce.
c. Xalibai ne.
d. Abdu babban mutum ne

e. Binta doguwa ce.

Idan ka duba jimla dirkau za ka ga cewa bayani take yi ko amsa ga wata tambaya a kan mutum ko wani abu. Misali, kamar a ce: Wane ne Abdu? Amsar kuma sai a ce 'Abdu sarki ne ko sarki ne'. A misali na (1c) 'dirka' *ne* ita ce a matsayin yankin bayani, amma a misali na (1d) 'babban mutum ne' duk yankin bayani ne mai qunshe da yankin suna na biyu ne ko kuma 'cikamako' da kuma *ne*. A tsarin jimla dirkau abin da ake dirkewa zai iya kasancewa 'suna' ko 'sifa' mai zuwa a matsayin suna. A kullum kalmomin 'dirka' suna dacewa ne da sunan da ake son tabbatarwa ko dirkewa, idan aka yi amfani da kalmar 'dirka' da ba ta dace ba, to jimlar za ta kasance ta sava da dokar nahawun daidaitacciyar Hausa. Misali, Abdu dogo ce*. Ka ga a nan kalmar *ce* a matsayin dirka ba ta dace da suna Abdu ba. Shi ya sa jimlar ta zama ba karvavviya ba.

### 3.1.2 Jimla Tambayau

Jimla tambayau nau'in jimla ne maras aikatau da take zuwa da sigar tambaya. Wani lokaci tana zuwa da alamar tambaya ko kalmar tambaya. Misali:

2a. Binta malama ce?

b. Abdu dogo ne?

c. Abdu mai wayo ne?

d. Wane ne wannan?

e. Wace ce malamar?

f. Mene ne launin rigar?

g. Motoci nawa ne a gidan?

Duk misalan da na bayyana maka a (2a-g) sun danganci jimla tambayau maras aikatau kuma duk suna xauke da kalmar dirka. Misali na (2a-c) sun kasance tambayau saboda alamar tambaya da ta zo a qarshe. Misali na (2d-f) sun kasance jimloli tambayau saboda amfani da aka yi da kalmomin tambaya *wane* da *wace* da *mene* da makamantansu. Kuma duk amsar da za a bayar ita ma tana kasancewa jimla maras aikatau. Misali amsar (2e) ita ce, 'Binta ce'. Haka ma misali na (2g) an yi amfani da kalmar tambaya *nawa*.

### 3.1.3 Nunau

Jimla nunau tana iya kasancewa maras aikatau, musamman ma nunau dogo. Kalmomin nunau dogo su ne kamar *wannan* ko *waccan* ko *waxannan* ko kuma *waxancan*. Misali:

3a. Wannan mota ce.

b. Waxannan motoci ne.

c. Waccan rigar baqa ce.

Duk misalan idan ka duba da kyau sun fara ne da kalmomin ‘nunau dogo’ kuma duk suna xauke da kalmomin ‘dirka’.

A nan zan iya faxa maka cewa duk jimloli marasa aikatau a Hausa ya zama dole a samu kalmar ‘dirka’ a ciki, ko da kuwa jimlar ba dirkau ba ce. Wannan ya zama gaskiya idan ka duba duk misalan da muka yi nazari. Bugu da qari, duk jimlolin da na yi maka bayani marasa aikatau za a iya mayar da su tsarin jimla korarriya. Wato a yi amfani da kalmomin korewa a cikin su kamar yadda ake yin amfani da su a tsarin jimla mai aikatau. Musamman kalmar korewa *ba*. Misali, idan ka xauki misali na (3a-c) za ka iya mayar da misalan korarru kamar haka:

4a. Wannan *ba* mota *ba*.

b. Waxannan *ba* motoci *ba* ne.

c. Waccan rigar *ba* baqa *ba* ce.

Kamar yadda ka gani a (4a-c) sauran jimlolin ma na (1-3) duk za su iya amfani da kalmar korewa *ba* .

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan nau’in jimla maras aikatau a nahawun Hausa. Na bayyana maka nau’in jimla maras aikatau kamar ‘dirkau’ da ‘tambayau’ da kuma ‘nunau’.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Jimla a nahawun magana ce mai tsari na musamman xauke da cikakkiyar ma’ana.
- Kuma kalmomin da suke a harshe su ne tubalan da ake yin amfani da su wajen gina ta.
- Kalmomin da ake harhaxawa su samar da jimla su ne rukunonin nahawun harshen.
- Akwai jimloli marasa aikatau kamar dirkau da tambayau da kuma nunau.
- Kalmomin ‘dirka’ sun taka muhimmiyar rawa a duk nau’o’in jimlolin.

- Jimlolin gaba xaya an gina su ne a kan qa’idar jinsi ta nahawun Hausa, duk inda aka yi amfani da ‘dirka’ *ne* to lallai jinsin namiji ko jam’i ake tabbatarwa, idan kuwa *ce* ta zo a jimlar za ka ga cewa jinsin mace ake tabbatarwa.

## Auna Fahimta

1. Ta wace hanya za ka bambance jimla dirkau da jimla tambayau?
2. Yaya za ka bayyana ‘yankin bayani’ a tsarin jimla maras aikatau?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Wacce irin rawa ‘dirka’ take takawa a ire-iren jimlolin Hausa marasa aikatau?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu’azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Bishiyar Li’irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 3 Tsarin Jimlar Hausa

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Tsarin Jimlar Hausa
3.1.1 Aikau + Aikatau + Karvau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayanin tsarin jimlar Hausa na gaba xaya. Wato ina so in faxa maka cewa kowane harshen a xan'adam an gina jimlolinsa masu xauke da aikatau a kan tsari na bai-xaya. An yi ittifaqin cewa jimloli masu 'aikatau' su ne mafiya rinjaye da suke bayyana tunanin xan-adam. Saboda haka tsarin jimla na harsunan duniya an gina shi ne a kan jimla mai aikatau. Kuma kowane harshe yana da nasa irin tsarin da masu magana da harshe suke bi wajen gina jimlolinsa. Harshen Hausa kamar yadda zan yi maka bayani nan gaba ana gina jimlolinsa masu aikatau a kan tsari na 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'. Bari na ba ka misali da harsunan da ka sani. Ka ga harshen Ingilishi jimlolinsa masu aikatau ana gina su ne a kan tsari na 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'. Amma shi kuwa harshen Larabci ana gina jimlolinsa a kan tsari na 'aikatau' da 'aikau' da kuma 'karvau'. Wannan kashi zai yi maka cikakken bayani a kan tsarin jimlar Hausa da abubwan da ta qunsa. Wato, 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da kai:

- Ginshiqan abubuwan da jimlolin Hausa masu aikatau suka qunsa. Wato, darasin zai maka bayanin tsarin da ake gina jimlar Hausa mai aikatau.
- Tsarin da darasin zai yi maka bayani shi ne 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Tsarin Jimlar Hausa

Masu magana da harshen xan’adam suna gina jimlolinsu musamman masu xauke da aikatau ta hanyar bin wani tsari na bai-xaya. Wannan tsarin shi ne yake nuna kamannin jimla a harshe. Wane tsari ake gina harsunan duniya a kai? Tsarin da ake gina harsunan duniya a kai shi ne ta hanyar duba aikin da rukunonin nahawu suke yi a harshen. Tsarin bai-xaya da ake xora harsunan duniya a kai shi ne ‘aikau’ da ‘aikatau’ da ‘karvau’, ko ‘aikatau’ da ‘aikau’ da ‘karvau’ ko kuma ‘karvau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘aikau’. Ko kuma a kan wani tsarin mai kama da waxannan da na faxa maka. Tambaya a nan ita ce, a kan wane tsari aka xora jimlolin Hausa masu xauke da aikatau? Amsa ita ce, ana gina jimlolin Hausa masu xauke da aikatau a kan tsari na ‘aikau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau’. Duk harsunan duniya da ‘yan’adam suke yin magana da su suna da makamancin wannan tsarin. Ana gane tsarin ne bayan an yi nazarin rukunonin nahawu da jimlolin harshen. Tunda na yi maka bayanin jimlolin Hausa da rukunoninsu, yanzu zan kawo maka bayani dangane da tsarin da aka xora jimlolin Hausa a kai. Bayanina zai mai da hankali kan abubuwa guda uku, su ne ‘aikau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau’.

### 3.1.1 Aikau + Aikatau + Karvau

Wannan sashen zai yi maka cikakken bayani kan ‘aikau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau. Daga nan kuma zan kawo maka misalai na jimloli masu irin wannan tsarin. Bari na fara da ‘aikau’. A tsari na nahawu idan aka ce ‘aikau’ me ake nufi? Idan aka ce ‘aikau’ a ilimin nahawu ana nufin wanda ya yi wani aiki da ya zo a cikin jimla. Wato, shi ne ‘ma’aikaci’, kuma ‘suna’ wanda yake zuwa a yankin suna na farko. Shi ne ‘suna’ da ya yi wani aiki ko aka danganta shi da akasin aiki a jimla. Ana samun ‘aikau’ a yankin suna na farko, ba yankin suna na biyu ba. Shi yankin suna na biyu yana zuwa ne qarqashin yankin bayani mai xauke da ‘aikatau’. Misalin jimloli masu xauke da ‘aikau’ su ne:

1a. <u>Abdu</u> ya mari Binta.
b. Wani <u>yaro</u> ya mari Binta.
c. Wani xan <u>yaro</u> baqi ya mari Binta.
d. Wani gajeren <u>yaro</u> baqi ya mari Binta.

Idan ka yi nazarin waxannan misalan (1a-d) za ka ga cewa an yi amfani da ‘suna’ a duk jimlolin an ja layi a qasansa. Wannan yana nuna cewa ‘Abdu’ shi ya kasance ‘aikau’ a jimla ta (1a), amma a (1a-d) ‘yaro’ shi ne ‘aikau’, kalmomin da suka zo

kafin ‘suna’ suna yin qarin bayani ne a kan ‘aikau’. Waxannan rukunan nahawu da suka zo kafin ‘aikau’ su ne a matsayin ‘sifatau na xaya’. Misali, (1d) ya qunshi sifatau da suka haxa da ‘mafayyaci’ da ‘sifa’ da ‘madanganci’, ‘yaro’ shi ne ‘aikau’. Idan aka cire ‘yaro’ sai jimlar ta zama ba karvavviya ba. Saboda haka rukunonin nahawu da suka zo kafin ‘suna aikau’ a matsayin sifatau da rukunonin da suka zo a bayan ‘suna aikau’ a matsayin ‘sifatau na biyu’ duk bayani suke yi a kan ‘suna aikau’. Dangin ‘suna’ su ne suke zuwa a matsayin ‘aikau’ kamar ‘wakilin suna’ da ‘nunau dogo’ da makamantansu. Idan ka fahimci ‘aikau’, to sai kuma mu matsa don yin bayanin aikin da ‘aikau’ yake yi a jimla, wato ‘aikatau’.

‘Aikatau’ shi ne rukunin da yake xauke da aikin da aka yi a cikin jimla. ‘Aikatau’ ko ‘fi’ili’ rukunin nahawu ne mai matuqar muhimmanci; domin shi ne ginshiqi a tsarin jimla. ‘Aikatau’ ba ya zuwa sai an samu ‘aikau’, shi kuma ‘aikatau’ ba ya zuwa sai da ‘zaginsa’ (shi ne ake kira zagin aikatau). ‘Aikatau’ shi ne ginshiqi a yankin bayani kamar yadda ‘aikau’ yake a yankin suna’. Abin da yake fara zuwa a yankin bayani shi ne ‘zagin aikatau’ daga shi sai gundarin ‘aikatau’. Misali na (a-d) suna xauke da ‘aikatau’ xaya ne shi ne *mari*, amma kafin ‘aikatau’ *mari* akwai zaginsa *ya*. Shi ‘aikatau’ yana iya sauya kamanni, amma dai duk kamanni da zai sauya yana zuwa ne bayan zaginsa. Misali:

2a. Abdu ya *karanta* shi.
b. Abdu ya *karanci* littafin.
c. Abdu ya *karance* littafin.
d. Abdu ya *karanto* shi.
e. Abdu ya *karantar* da su.
f. Abdu ya *karantu*.

A nan ina so na nuna maka cewa ‘aikatau’ yana sauya kamanni gwargwadon yadda ya zo a jimla. Haka kuma ‘aikatau’ iri biyu ne kamar yadda na yi maka bayani tun da farko. ‘Aikatau so-karvau’ wannan shi ne ‘aikatau da yake zuwa da karvau kamar yadda na misalta a (2a-e). ‘Aikatau qi-karvau’ shi ne ‘aikatau’ xin da ba ya zuwa da karvau a bayansa, kamar a misali na (2f). Yawanci ‘aikatau’ a Hausa so-karvau ne. Shi ya sa tsarin jimlar Hausa ya kasance ‘aikau’ da ‘aikatau’ da kuma ‘karvau’. Yanzu kuma sai tsarin jimlar Hausa na qarshe da ake kira ‘karvau’.

Bayan ka fahimci wanda ya yi aiki da kuma aikin da aka yi akwai kuma buqatar ka san matsayin aikin. Karvau tsari ne na ginuwar jimla da daidaituwarta. Karvau shi ne vangaren nahawu da aiki yake faxa wa kan sa. Karvau zai iya kasancewa ‘suna’ kamar yadda na ba ka misalta maka a (1a). Aikin mari da ‘Abdu’ ya yi ya faxa kan ‘Binta’. Shi ya sa ‘Binta’ ta zama ‘karvau’. Kamar yadda ‘aikau’ zai iya kasancewa

'wakilin suna' haka ma 'karvau' kamar yadda na nuna maka a (2a), kalmar *shi* a nan ita ce 'karvau' xin. 'Karvau' a Hausa iri biyu ne. Akwai 'karvau kai tsaye' da kuma 'karvau kaikaice'. Duba waxannan misalan don ka rarrabe su:

3a. Binta ta dafa *abinci*. (abinci, karvau kai tsaye)

b. Binta ta dafa wa *yara abinci*. (yara, karvau kaikaice)

A misali na (3a) aikin da aka yi a jimlar ya faxa kan 'karvau' *abinci*. Saboda haka *abinci* shi ne karvau kai-tsaye. Kuma a (3a) idan ka lura za ka ga 'suna' xaya ne ya biyo 'aikatau' *dafa*. Amma a (3b) 'aikatau' *dafa-wa* (mai xauke da xafin -wa) suna biyu ne suka biyo shi. Sunan da ya fara zuwa shi ne 'karvau kaikaice', *abinci* har yanzu shi ne sunan da kai tsaye ya karvi aikin da aka yi. Haka lamarin yake jimlolin Hausa sukan zo da 'karvau' xaya ko biyu.

Tunda ka fahimci tsarin jimlar Hausa daga 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau', yanzu zan nuna maka su a tsarin jimlar Hausa. Ga misalin jimlolin:

4. Abdu ya mari Binta.

Aikau — Aikatau — Karvau

Duk qarin da aka yi wa jimlar ba zai sauya tsarin nahawun jimlar ba. Misali:

5. Wani farin mutum dogo ya mari wata yarinya doguwa.

Yankin Suna — Yankin Bayani

Mutum (Aikau) — Aikatau — Yarinya (Karvau)

Yanzu bari na nuna maka wani misalin mai xauke da karvau guda biyu.

6. Abdu ya xinka wa Binta riga

Yankin Suna — Yankin Bayani

Abdu (Aikau) — Aikatau — Karvau Kaikaice — Karvau Kai-tsaye

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashin na yi maka bayani kan tsarin da ya kevanta ga jimlolin Hausa musamman masu 'aikatau'. Tsarin da ya kevanta ga jimlolin shi ne 'aikau' da 'aikatau' da kuma 'karvau'. Na kawo maka bayaninsu daki-daki haxe da misalai.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- jimla mai xauke da aikatau a nahawun Hausa tana da wani tsari da ya kevanta da ita.
- Tsarin shi ne a gabatar da wanda ya yi aiki (aikau) da aikin da aka yi (aikatau) da kuma wanda ya karvi aikin (karvau).
- 'Aikau' da 'karvau' za su iya zuwa a matsayin 'suna' ko 'wakilin suna'.
- Sauya kamanni da aikatau yake yi a jimla ba ya sauya tsarin jimlar Hausa.
- 'Karvau' iri biyu ne akwai na kai-tsaye da kuma na kaikaice. Duk kuma za su iya kasancewa a jimla guda.

## Auna Fahimta

1. Bayyana tsarin jimlar Hausa mai aikatau.
2. Ta yaya za ka bambance 'aikau' da 'aikatau' a tsarin jimlar Hausa?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Wacce irin rawa 'karvau' yake takawa a tsarin jimla mai aikatau?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari

Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

Kashi Na 4 Qarfafawa

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Ma'anar Qarfafawa
3.2 Ire-iren Qarfafawa
3.2.1 Qarfafawa Ta Jigo
3.2.2 Qarfafawa Kevantau
3.2.3 Qarfafawa Bambantau
3.2.4 Qarfafawa Rikixau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

## 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayanin qarfafawa da nau'o'inta a nahawun Hausa. Wato ina so in faxa maka cewa kowane harshe na xan'adam yana yin amfani da tsari na qarfafawa a zubin jimlolinsa. Qarfafawa yanki ce na nahawu da take taimakawa wajen ba da fifiko a magana. Kalmomin qarfafawa ba sa qarya qa'idar nahawun harshe ko tsarin ginin jimla. Wani lokaci masu magana da harshe suna son nuna muhimmanci ko fifiko ga wani vangare na harshe, qoqarin yin haka shi ya haifar da 'qarfafawa' a nahawu. Kowane harshe yana da hanyoyin da yake bi wajen nuna fifiko ko muhimmanci ga wani sashe na jimla ko jimlar gaba xaya. Haka ma harshen Hausa ba a bar shi a baya ba wajen qarfafa zance a tsarin jimla. Ya kamata ka sani cewa kamar yadda ake da kalmomin 'aikatau' da na 'bayanau' da na 'nunau' da na 'mafayyaci' a Hausa, haka ma 'qarfafawa' tana da irin nata kalmomin da in har suka zo cikin jimla to lallai an nuna fifiko ga wani abu ko sashe na jimlar. Samun wannan shi ya tabbatar da cewa 'qarfafawa' a nahawun iri-iri ce a Hausa. Wannan kashi zai fito maka da su tare da bayaninsu daki-daki.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce:

- koyar da kai qarfafawa a nahawun Hausa.
- Yadda ake nuna fifiko ga wani sashe na jimla ko ma jimlar kanta ta hanyar yin amfani da kalmomin qarfafawa.
- Fito maka da ire-iren qarfafawa a tsarin jimlolin Hausa.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Ma'anar Qarfafawa

'Qarfafawa' wani sashe ne na nahawun da yake da matuqar muhimmanci a ilimin kimiyyar harshe. Masu magana da harshen xan'adam suna gina jimlolinsu ta hanyar bin wani tsari na bai-xaya, qarfafawa tana xaya daga cikin wannan tsarin. Saboda masu magana da harshe sukan nuna ko bayyana fifiko a kan wata kalma ko wani vangare na jimla ko ma jimlar gaba xaya. Wannan fifikon shi ne abin da ya danganci 'qarfafawa'. To, a ilimin nahawu me ake nufi da 'qarfafawa'. 'Qarfafawa kamar yadda Sani (1999: 94) ya bayyana "tana nufin ba da fifiko ko muhimmanci na musamman a kan wani vangare na jimla ko jimlar gaba xayanta a lokacin magana". Wannan ma'anar ita take nuna cewa akwai ire-iren qarfafawa a tsarin nahawun Hausa. Yanzu zan gabatar maka da ire-iren qarfafawa xaixai-da-xaixai tare da misalansu.

## 3.2 Ire-iren Qarfafawa

Kafin na gabatar maka da ire-iren qarfafawa ya kamata na tuntar da kai cewa qoqarin bayar da fifiko ga wani yanki na jimla ko jimlar gaba xaya shi ya haifar da 'qarfafawa' da ire-irenta a nahawun Hausa. Zan bi ire-iren qarfafawa da Sani (1999: 94-98) ya bayyana kamar haka:

i. Qarfafawa ta jigo
ii. Qarfafawa kevantau
iii. Qarfafawa bambantau
iv. Qarfafawa rikixau

### 3.2.1 Qarfafawa Ta Jigo

Wannan nau'i ne na 'qarfafawa' da ake yin amfani da kalmomin qarfafawa kamar *fa* da *ko* da *dai* da *kuwa* da *ma* da dangoginsu. A irin wannan qarfafawa za a iya qarfafa kowane vangare na jimla. Misali:

1a. Abdu ya mari Binta xazu.

b. Abdu *fa* ya mari Binta xazu.

c. Abdu ya *fa* mari Binta xazu

d. Abdu ya mari *fa* Binta xazu.

e. Xazu *fa* Abdu ya mari Binta.

f. Abdu ya mari Binta xazu *fa*.

g. Binta *kam,* Abdu ya mare ta.

Kamar yadda na sanar da kai cewa irin wannan qarfafawa tana yin amfani da qarfafau ne wajen yin ta kuma ana iya qarfafa kowane vangare na jimla. Yanzu bari na yi maka bayanin qarfafau da na misalta maka a (1a-f). Idan ka duba misalan za ka gane cewa misali na (1a) ba shi da qarfafau, jimla ce sakakkiya, amma a misali na (1b) za ka ga an qarfafa wanda ya yi aiki ne , wato ‘aikau’ Abdu. Saboda qarfafau *fa* ta zo bayan ‘aikau’. A misali na (1c) an qarfafa ‘zagin aikatau’ *ya*, kamar yadda ka gani qarfafau ta biyo ‘zagin aikatau’. Idan qarfafau xin ta biyo ‘aikatau’ kamar a (1d), to an qarfafa ‘aikatau’ ne. Idan kuwa ‘bayanau’ ake son qarfafawa to sai an kawo shi farkon jimlar kamar yadda ka gani a (1e), a nan an qarfafa ‘bayanau’ *xazu*. Kai, in taqaice maka, jimla ma gaba xaya za a iya qarfafa ta. Duba misali na (1f), a nan ka ga qarfafau xin *fa* ta zo a qarshen jimlar, wannan shi yake nuna cewa jimlar kacokan aka qarfafa. A nan na san z aka yi tambaya kan, yaya tsarin qarfafa ‘karbau’ yake? Amsar dai ita ce idan ka duba misali na (1a) za ka ga cewa Binta ita ta zo a matsayin ‘karvau’, idan za a qarfafa ta sai a turo ta farkon jimlar kamar yadda yake a (1g) kuma qarfafau ta biyo ta. Sannan akwai yiwuwar a kawo ‘wakilin suna’ a qarshe da ya dace da ‘karvau’ xin kamar yadda na nuna maka a (1g). Bisa al’ada akan xan dakata bayan an faxi qarfafau, za ka ga na sa waqafi a bayan qarfafau. Wani zai iya cewa ‘Binta *kam,* Abdu ya mara’. Wannan shi ne bayani kan qarfafawa ta jigo ko manufa. Yanzu sai kuma qarfafawa kevantau.

### 3.2.2 Qarfafawa Kevantau

Ga yadda Sani (1999: 96) ya bayyana ‘qarfafawa kevantau’ da misalinta kamar haka “Qarfafawa kevantau ita kuwa ana yin amfani da Shuxaxxen Lokaci na II wajen yin ta”. An kira ta da wannan suna ne saboda keve wani abu ake yi daga wani. Misali:

2a. Xalibai sun gama jarrabawa jiya.

b. Xalibai (ne) suka gama jarrabawa jiya.

c. Xalibai (ne) suka gama jarrabawa jiya, ba malamai ba.

d. Jarrabawa (ce) xalibai suka gama jiya.

e. Jiya (ne) xalibai suka gama jarrabawa.

Idan ka duba misali na (2a) jimla ce sakakkiya babu wani batu na qarfafawa a cikin ta. Sauran misalan (2b-e) duk sun danganci qarfafawa. Ka ga a (2b) an qarfafa ‘aikau’ na jimlar wato *xalibai*, kalmar dirka (ne) a cikin baka ganin dama ne za a iya cire ta ba tare da haifar da wata matsala ba. Ida nana son a qarfafa keve xalibai daga malamai, to sai ka duba misali na (2c). Idan kuwa ‘karvau’ jarrabawa ake son a qarfafa, sai ka duba misali na (2d), wato dai sai ka turo ‘karvau’ jarrabawa zuwa farkon jimlar. Wato yana da kyau ka gane cewa ‘karvau’ da ‘bayanau’ ana bas u fifiko ta hanyar kawo farfon jimla. Ka ga (2e) misali ne da aka qarfafa bayanau. Tunda ka fahimci qarfafawa kevantau yanzu sai mu juya ga qarfafawa bambantau.

### 3.2.3 Qarfafawa Bambantau

Qarfafawa bambantau ta qunshi yin amfani da kalmar *sai* a farkon jimla. Misali:

3a. Abdu zai wanke motar yau.

b. *Sai* Abdu zai wanke motar yau

c. *Sai* motar Abdu zai wanke yau.

d. *Sai* yau Abdu zai wanke motar

Idan ka duba da kyau za ka ga cewa a jimlar da take a misali na (3a) ba ta da qarfafawa, amma jimlar da ta zo a (3b) tana da qarfafawa, an kuma qarfafa ‘aikau’ xin jimlar ‘Audu’. A misali na (3c) an qarfafa ‘karvau’ motar, saboda ita aka ba wa fifiko. A misali na (3d) kuwa an qarfafa kalmar ‘bayanau’ yau. A irin wannan qarfafawa ba a yin ta ga jimla.

### 3.2.4 Qarfafawa Rikixau

Kamar yadda sunanta ya nuna qarfafawa tana haifar da rikixewar jimla gaba xaya. Wato, a nan jimlar da aka gina bisa Lokaci Na Yanzu Na 1 tana rikixewa zuwa Lokaci Na Yanzu Na II (nan gaba kaxan zan yi maka bayani kan lokutan Hausa). Misali, idan aka ce, ‘Binta tana wanki’. Wannan jimla ce maras qarfafawa kuma an gina ta a tsarin lokaci na yanzu na xaya, za ta iya rikixewa zuwa lokaci na yanzu na biyu kamar haka: ‘Binta wanki take yi’. A wannan misalin Binta ‘suna aikau’ ake qarfafawa. Amma idan aka ce: ‘Wanki Binta take yi’, a nan ana qarfafa *wanki* ‘suna xan aikatau’. Muhimmin abu dai a nan shi ne rikixewa da take aukuwa daga Lokaci Na Yanzu Na 1 zuwa Lokaci Na Yanzu Na II.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan ma'anar qarfafawa da hanyoyin da ake bi wajen qarfafa wani vangare na jimla ko jimlar gaba xaya. Dangane da haka mun yi nazarin nau'o'in qarfafawa har guda huxu da suka haxa da qarfafawa ta jigo da qarfafawa kevantau da bambantau da kuma rikixau tare da misalan kowacce.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Qarfafawa tana da matuqar amfani a nahawun Hausa.
- 'Qarfafawa' hanya ce ta nuna fifiko ga wani yanki na jimla ko jimla gaba xaya, ana yin amfani da qarfafau kamar *fa* da *kam* da *ko* da *ma* da makamantansu.
- Akwai iri huxu na qarfafawa a Hausa, su ne qarfafawa ta jigo da qarfafawa kevantau da qarfafawa bambantau da kuma qarfafawa rikixau.
- 'Qarfafawa' ta jigo za a iya qarfafa duk rukunan da suka zo a jimla.
- Tsarin qarfafa 'karvau' da 'bayanau' ya bambanta da yadda ake qarfafa sauran rukunan nahawu na jimla.

## Auna Fahimta

1. Me ya sa qarfafawa ta 'karvau' da 'bayanau' ta zama ta daban?
2. Ta wace hanya ake qarfafa wani yanki na jimla?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Bayyana muhimmancin 'qarfafawa' a nahawun Hausa.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

Kashi Na 5 Ganga

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Ma'anar Ganga
3.2 Ire-iren Ganga
3.2.1 Ganga Dogarau
3.2.2 Ganga Tsayayyiya
3.3 Matsayin Ganga A Nahawu
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

## 1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayanin 'ganga' a nahawun Hausa. Ka sani cewa kowane harshe na xan'adam yana da wasu abubuwa da suka kevanta da shi waxanda suka danganci ginin jimla. Daga cikin abubuwan da harshen Hausa ya kevanta da su akwai abin da ake kira 'ganga'. 'Ganga' kamar yadda sunan yake ba ana nufin ganga ta kixa ba. Ganga rukunin kalmomi ne da suka danganci ginin jimla. Shi ganga kamar yadda masana suke bayyana shi bai kai cikar jimla ba amma kuma yana xauke da 'aikatau'. Wannan yana nuna maka cewa yana da muhimmanci a nahawun Hausa. Domin duk abin da za a ce yana qunshe da 'aikatau' to lalle ya zama abin dubawa da nazari. Shi 'ganga' kamar yadda za ka gani ya qunshi wani yanki ne a jimla wanda shi kaxai ba zai bayar da cikar jimla ba sai an haxa da wani vangaren. Irin jimla mai xauke da 'ganga' takan xauki kalmomin aikatau guda biyu. A taqaice dais hi 'ganga' ba ya zuwa a matsayin kalma guda. Amma fa yana da muhimmanci a nahawun Hausa domin zai iya zuwa a matsayin 'aikau' ko 'bayanau' ko kuma 'cikamako'. A wannan kashi zan gabatar maka da ma'anar 'ganga' da ire-irensa da misalansa a cikin jimloli.

## 2.0 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi:

- za ka san abin da ake kira ‘ganga’ da nau’o’insa da kuma irin rawar da yake takawa a nahawun Hausa.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

### 3.1 Ma’anar Ganga

‘Ganga’ wani jerin kalmomi ne bisa tsari mai xauke da aikatau wanda bai kai cikar jimla ba. Misalin ganga shi ne kamar a ce ‘*da suka tafi* ko *inda na san shi* da makamantansu. Sashe na gaba zai yi maka bayani kan ire-iren ganga a Hausa.

### 3.2 Ire-iren Ganga

‘Ganga’ a nahawun Hausa ya kasu gida biyu. Akwai ‘ganga dogarau’ da kuma ‘ ‘ganga tsayayyiya’. Waxannan ire-iren ganga su suke nuna yadda ‘ganga’ yake taka rawa a matsayin ‘aikau’ ko ‘bayanau’ ko kuma ‘cikamako’. Yanzu ga bayaninsu daki-daki.

#### 3.2.1 Ganga Dogarau

‘Ganga dogarau’ nau’i ne na ‘ganga’ wadda ba ta iya zama ita kaxai a tsari na jimla sai ta dogara da wani abin daban. Wannan shi ne dalilin kiran ta da ‘ganga dogarau’. Misali:

1a. Ya zo *bayan sun tashi*.
b. Sun shiga *da aka kira su*.
c. Za mu saya *in an samu*.

Sani (1999: 88) ya ce “*bayan sun tashi* da *da aka kira su* da *in an samu* kowannensu yana matsayin ‘ganga dogarau’ ne. Kowanne ka xauka shi kaxai ba zai zauna ba. Shi ya sa ‘ganga’ ta jimlar (1a) ta dogara da *ya zo,* ta (1b) ta dogara da *sun shiga,* ta (1c) kuma da *za mu* saya. Yanzu kuma sai mu tafi ga ‘ganga tsayayyiya.

#### 3.2.1 Ganga Tsayayyiya

‘Ganga tsayayyiya’ kamar yadda sunanta ya nuna ita tana iya tsayawa da kanta ba tare da ta jingina da wani abu ba. Kamar yadda Sani (1999: 89) ya bayyana misalin da aka gabatar a (1a-c) suna xauke da nau’in ‘ganga tsayayyiya’, *ya zo* a misali na (1a), da *sun shiga* a misali na (1b) da kuma *za mu saya* duk misalai ne na ‘ganga tsayayyiya’ domin za ka iya faxar su ka yi shiru ba tare da wata matsala.

Qarin bayani da zan yi maka a nan shi ne duk nau’o’in suna xauke da ‘aikatau’, sai adai ‘aikatau’ na ‘ganga dogarau’ ya dogara da ‘aikatau’ na ‘ganga tsayayyiya’. Wannan yana nuna maka cewa duk nau’o’in za su iya zuwa a tsarin jimla guda.

## 3.3 Matsayin Ganga a Nahawu

Dangane da yadda ake yin amfani da ‘ganga dogarau’ da kuma ‘ganga tsayayyiya’ a nahawun Hausa, ‘ganga’ za ta iya zuwa a matsayin ‘aikau’ da matsayin ‘karvau’ da matsayin ‘bayanau’ da kuma matsayin ‘cikamako’ (duba aikin Sani, 1999: 89). Misali:

2a. Waxanda suka zo sun koma.

Aikau

Wasu misalan da ‘ganga’ take zuwa a matsayin ‘aikau’, wato wanda ko waxanda suka yi aiki a jimla, su ne:

3a. Wanda ya zo ya koma.

b. Wadda ta haihu ta tafi.

A nan jerin kalmomin da aka ja layi a qasansu misalai ne na ‘ganga dogarau’ a matsayin ‘aikau’. Haka kuma su ma jerin kalmomin ‘ganga tsayayyiya’ sukan zo a mtsayin ‘aikau’ kamar yadda za ka gani a misali na (4a-c) (don qarin bayani sai ka duba aikin Sani, 1999: 98-90).

4a. *A gudu* ya fi a tsaya.

Aikau

b. *A ci* ya fi a zubar.

c. *An bayar* ya fi an sace.

Haka kuma ‘ganga’ yana iya zuwa a matsayin ‘karvau’. Misali:

5a. Mun san *waxanda suka zo.*

Karvau

b. Ta san *wadda ta tafi*.

c. Sun ga *yadda suke yi*

A waxannan misalan kalmomin da suka haxu a matsayin karvau su ne a (5a) *waxanda suka zo*, a (5b) *wadda ta tafi*, a kuma (5c) *yadda suke yi.*

Har ila yau, akwai wasu wuraren da 'ganga' take zuwa a matsayin cikamako. 'Cikamako' kamar yadda ka yi nazari a baya yana zuwa a matsayin yankin suna ne kamar a ce 'Abdu *babban mutum ne*'. To baya ga wannan, 'cikamako' yana iya zuwa ma a matsayin 'ganga'. Duba waxannan misalan da (Sani 1999: 91) ya gabatar:

6a. Sun tafi *inda suka fito*.

Cikamako

b. Mun dawo *wurin da aka haife mu*.

c. Ya koma *inda aka umarce shi*.

Idan ka duba wxannan misalan za ka ga cewa *inda suka fito* da *wurin da aka haife mu* da kuma *inda aka umarce shi*; duk misalai ne na ganga dogarau a matsayin 'cikamako'. Duk suna xauke da ma'anar 'wuri'. Bugu da qari, ganga tsayayyiya ma tana iya zuwa a matsayin cikamako. Duba misali na (7):

7a. Sun tafi *su kama kifi.*

Cikamako

b. Ta dawo *ta kalle su*.

c. Ya koma *ya rubuta su.*

Haka ma lamarin yake a nan, idan ka duba misalan da suka zo *su kama kifi* da *ta kalle su* da kuma *ya rubuta su* duk misalai ne na 'ganga tsayayyiya' a matsayin 'cikamako'. Duk misalan suna da alaqa da wani dalili. Misali, dalilin *tafiya* da na *dawowa* da kuma na *komawa*.

Yanzu kuma zan nuna maka 'ganga' a matsayin 'bayanau'. Ga yadda Sani (1999: 92) ya kawo bayanin 'ganga' a matsayin 'bayanau'. Ita ganga za iya danganta ta da lokaci ko sharaxi ko wuri ko yanayi wani lokaci ma har da zavi. Ga misalansu kamar haka:

8a. Sun zo *bayan mun tashi* ('ganga a matsayin 'bayanau' na lokaci).

b. Ba zai sake zuwa ba *har ya mutu* ('ganga bayanau na lokaci').

c. Ba ta yi ciwo ba *tun da aka haife ta* ('ganga bayanau na lokaci').

9a. Za su yi fushi *idan aka vata musu rai* ('bayanau na sharaxi').

b. Za mu saya *muddin muka samu kuxi* ('bayanau na sharaxi').

c. Za a kama shi *idan an gan shi* ('bayanau na sharaxi').

10a. Ta gan su *wurin da suke zaune* ('bayanau na wuri').

b. Ta bi shi *wurin da yake aiki* ('bayanau na wuri').

c. An raka ta *inda za ta tafi* ('bayanau na wuri').

11a. Sun yi shi *yadda muke so* ('bayanau na yanayi').

b. Za mu ba su *yadda aka umarce mu* ('bayanau na yanayi').

c. Mun kiyaye da shi *yadda aka ce* ('bayanau na yanayi').

Idan ka duba za ka ga cewa misalan da na kawo maka tun daga na (8) har zuwa na (11) nau'i ne na 'ganga' da yake zuwa a mtsayin 'bayanau'. 'Ganga' a matsayin bayanau iri-iri ce akwai 'ganga bayanau na lokaci' kamar yadda na nuna maka a (8a-c), ana gane shi da hakan idan kalmar *bayan* ko *har* ko *tun* ta zo a farkon zubin ganga. Haka za ka samu a misali na (8a-c). Misalai na (9a-c) kuwa sun qunshi 'ganga bayanau na sharaxi'. Su kuma ana gane su idan kalmar *idan* ko *muddin* ta zo a farkon Zubin ganga. Za ka haka lamarin yake daga misali na (9a-c). Misali na (10) 'ganga bayanau na wuri' ya qunsa. Ana gane su idan aka samu *wurin da* ko *inda* sun zo a farkon Zubin 'ganga'. Shi ma misali na (11a-c) 'ganga' ce a mtsayin 'bayanau na yanayi', ana gane su da wannan suna idan kalmar *yadda* ta zo a farkon zubin 'ganga'.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan:

- ma'anar 'ganga' da nau'ointa da hanyoyin da ake bi wajen gane matsayin 'ganga' a tsarin nahawun jimla.
- Na kawo maka bayani kan 'ganga dograu' da kuma 'ganga tsayayyiya.
- Yadda 'ganga' take taka rawa a matsayin 'aikau' da 'karvau' da 'cikamako' da kuma 'bayanau'.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- 'ganga' wani jerin kalmomi ne wanda bai kai cikar jimla ba mai kuma xauke da aikatau.
- Akwai 'ganga' wadda take iya dogara da kanta ita ake kira 'ganga tsayayyiya' da kuma 'ganga dogarau' wadda sai ta jingina da wasu kalmomin.
- Ka gane cewa duka nau'o'in za su iya zuwa a cikin jimla guda.
- Dangane da aikin 'ganga' a cikin jimla, tana iya yin aiki a matsayin 'aikau' da 'karvau' da 'cikamako' da kuma 'bayanau.

## Auna Fahimta

1. Me ka fahimta da 'ganga'?
2. Wane irin aiki ganga take takawa a cikin jimla?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Bayyana kamanci da bambanci tsakanin 'ganga dogarau' da kuma 'ganga tsayayyiya a nahawun Hausa.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu’azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu’azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi’u Muhammad. Bishiyar Li’irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2001.

**RUKUNI NA 3**

Kashi Na 1 Lokutan Hausa 1

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Ma'anar Lokaci
3.2 Lokutan Hausa 1
3.2.1 Shuxaxxen Lokaci Na I
3.2.2 Shuxaxxen Lokaci Na II
3.2.3 Lokaci Na Sabo
3.2.4 Lokaci Na Yanzu Na I
3.2.5 Lokaci Na Yanzu Na II
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

## 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zai yi maka bayanin lokuta a nahawun Hausa. Ka sani cewa kowane harshe na xan'adam yana da wasu abubuwa da suka kevanta da shi waxanda suka danganci ginin jimla. Daga cikin abubuwan da harshen Hausa ya kevanta da su akwai abin da ake kira 'Lokaci'. 'Lokaci' kamar yadda sunan yake nunawa ba ana nufin lokaci na agogo ba. 'Lokaci' yana da matuqar muhimmanci a ilimin nahawu. Saboda in dai an yi maganar jimla to lallai a duba batu kan 'lokaci'. Kowane harshe yana da nasa irin lokacin da ake danganta su da ginin jimla a harshe. Hausa tana da tsarin lokuta har guda takwas (Galadanci, 1976 da Bello, 2014). Saboda ka fahimci zubi da tsarinsu yadda ya kamata na raba maka su zuwa gida biyu. Kashi na farko ya qunshi 'shuxaxxen lokaci na I' da 'shuxaxxen lokaci na II' da 'lokaci na sabo' da 'lokaci na yanzu na I' da kuma 'lokaci na yanzu na II'. Kashi na biyu kuwa ya qunshi 'lokaci na gaba na I' da 'lokaci na gaba na II' da kuma 'umurtau' ko 'wanin lokaci'. A wannan kashin zan gabatar maka da guda biyar xin kashi na farko.

## 2.0 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi ana so ka fahimci:

- Ma’anar lokaci.
- Zubi da tsarin lokutan Hausa guda biyar.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

### 3.1 Ma’anar Lokaci

Sani (1999: 71) ya bayyana ma’anar ‘lokaci’ da cewa “Sa’ar wanzar da aiki ne na cikin jimla. Aiki zai iya kasancewa an wanzar da shi ya wuce, ko ana wanzar da shi a halin yanzu, ko kuma za a wanzar da shi a nan gaba. Misali, *Ya wanke rigarsa*, ko *Yana wanke rigarsa*, ko kuma *Zai wanke rigarsa*”. Shi kuwa Bello (2014: 57) cewa ya yi “Lokaci a Hausa na iya zama wani zamani da aka yi abu ko za a yi shi abin, ko kuma ake yin sa”. Daga waxannan ma’anoni za ka gane cewa ‘lokaci’ dai yana nufin yadda wani aiki ya gudana a cikin jimla. Saboda haka ‘lokaci’ yana da matuqar muhimmanci wajen ginin jimla.

### 3.2 Lokutan Hausa I

Lokuta nawa ne a Hausa? Galadanci (1976) da Jinju (1980) da Sani (1999) duk sun nuna cewa akwai lokuta guda takwas a Hausa. Waxannan lokutan su ne:

- Shuxaxxen lokaci na I
- Shuxaxxen lokaci na II
- Lokaci na sabo
- Lokaci na yanzu na I
- Lokaci na yanzu na II
- Lokaci na gaba na I
- Lokaci na gaba na II
- Umurtau / Wanin lokaci

To, yanzu kuma sai mu duba hanyar da ake bi wajen gane lokaci a Hausa. Ana gane 'lokaci' ta hanyar amfani da ‘wakilin suna’ ko ‘zagin aikatau’ mai xauke da karin sauti iri xaya (karin sauti shi ne kaifin sauti ko murya da ake danganta shi ga kowace gava. Hausa tana da karin sauti iri uku, akwai na sama da na qasa da kuma faxau. Ana sanya alamar karin sauti a kan wasalin farko na gaba) da ‘manunin lokaci’ da kuma ‘aikatau’. Ka ga wannan hanyar tana nuna maka cewa jimla maras ‘aikatau’ ba ta nuna ‘lokaci’. A baya na yi maka bayanin ‘wakilin suna’ da ‘zagin aikatau’, abin da ba ka gane ba kawai ‘manunin lokaci’. ‘Manunin lokaci’ shi ne yake da alhakin fayyace kowane irin lokaci ne ake yin magana a kai. Yanzu wannan kashin zai yi maka bayani a kan lokuta kashi na xaya, wato lokuta guda biyar da suka haxa

da ‘shuxaxxen lokaci I’ da ‘shuxaxxen lokaci na II’ da ‘lokaci na sabo’ da ‘lokaci na yanzu na I’ da kuma ‘lokaci na yanzu na II’. Kowane lokaci yana xauke da siga kamar haka; mai magana na farko da mai magana na biyu ko ta biyu da mai magana na uku ko ta uku da masu magana na farko da masu magana na biyu da kuma masu magana na uku.

### 3.2.1 Shuxaxxen Lokaci na I

‘Shuxaxxen Lokaci na I’ nuni yake yi da cewa an wanzar da aiki. Wato aikin da yake cikin jimla an yi shi ya wuce. ‘Shuxaxxen lokaci na I’ yana da tsari kamar haka:

i. zagin aikatau da karin sautin sama
ii. manunin lokaci -á (koyaushe da karin sautin sama) da kuma -n
iii. aikatau

Duba wannan jadawalin don ka ga tsarinsa tare da misalai:

Shuxaxxen Lokaci Na I

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | na | á | Rubuta | náá rubuta |
| Na biyu | ka | á | Rubuta | káá rubuta |
| Ta biyu | ki | n | Rubuta | kín rubuta |
| Na uku | ya | á | Rubuta | yáá rubuta |
| Ta uku | ta | á | rubuta | táá rubuta |
| Na farko jam’i | mu | n | rubuta | mún rubuta |
| Na biyu jam’i | ku | n | Rubuta | kún rubuta |
| Na uku jam’i | su | n | Rubuta | sún rubuta |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa manunin lokacin ‘shuxaxxen lokaci na I iri biyu ne, akwai -á (koyaushe yana zuwa da karin sautin sama) da kuma

-n (wannan ba shi da karin sauti, sai dai a wasalin da ya gabace shi). Dangane da manunin lokaci idan aka ce ‘náá rubuta’ manunin lokacin shi ne á, idan kuma cewa ka yi ‘mún rubuta’. To sai a ce *mu* a matsayin zagin aikatau sai n a mtsayin ‘manunin lokaci’. Haka kuma za a iya yin misali ba tare da an danganta da wani mai magana ba kamar a ce, ‘án rubuta’.

### 3.2.2 Shuxaxxen Lokaci na II

‘Shuxaxxen Lokaci na II’ shi ma nuni yake yi da cewa an wanzar da aiki. Wato aikin da yake cikin jimla an yi shi ya wuce. Duba wannan jadawalin don ka ga tsarinsa:

Shuxaxxen Lokaci Na II

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | na | - | rubuta | (ni ne) *na rubuta* |
| Na biyu | ka | - | rubuta | (kai ne) *ka rubuta* |
| Ta biyu | ki | ka | rubuta | (ke ce) *kíkà rubuta* |
| Na uku | ya | - | rubuta | (shi ne) *ya rubuta* |
| Ta uku | ta | - | rubuta | (ita ce) *ta rubuta* |
| Na farko jam’i | mu | ka | rubuta | (mu ne) *mukà rubuta* |
| Na biyu jam’i | ku | ka | Rubuta | (ku ne) *kukà rubuta* |
| Na uku jam’i | su | ka | rubuta | (su ne) *sukà rubuta* |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa manunin lokacin ‘shuxaxxen lokaci na II’ shi ne *kà* (koyaushe wasalin -a yana zuwa da karin sautin qasa), wasu zagagen aikatau xin ba su da manunin lokaci kamar yadda ka gani. Wani misalin da

ba ka gani a jadawalin ba shi ne na yin amfani da zagin aikatau da ba a danganta shi da wani mai magana ba kamar a ce ‘akà rubuta’.

### 3.2.3 Lokaci Na Sabo

‘Lokaci na sabo’ kamar yadda sunansa yake ya danganci aiki wanda aka saba yin sa. Wato aikin da ya zo a cikin jimla aiki ne da aka saba gudanar da shi. ‘Lokaci na sabo’ yana da tsari kamar haka:

i. ‘zagin aikatau’ da karin sautin sama
ii. ‘manunin lokaci’ -*kàn*
iii. ‘aikatau’.

Duba wannan jadawalin don ka ga tsarinsa:

Lokaci Na Sabo

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | ná | kàn | rubuta | nákàn rubuta |
| Na biyu | ká | kàn | rubuta | kákàn rubuta |
| Ta biyu | kí | kàn | rubuta | kíkàn rubuta |
| Na uku | yá | kàn | rubuta | yákàn rubuta |
| Ta uku | tá | kàn | rubuta | tákàn rubuta |
| Na farko jam’i | mú | kàn | rubuta | múkàn rubuta |
| Na biyu jam’i | kú | kàn | rubuta | kúkàn rubuta |
| Na uku jam’i | sú | kàn | rubuta | súkàn rubuta |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa manunin lokacin ‘lokaci na sabo iri xaya ne. Idan za ka ba da misali da zagin aikatau da ba a alaqanta shi da wani mai magana ba sai ka ce ‘ákàn rubuta’.

### 3.2.4 Lokaci Na Yanzu Na I

‘Lokaci na yanzu na I’ nuni yake yi da aikin da yake gudana a halin da ake ciki. Shi kuma ga yadda tsarinsa yake. ‘Wakilin suna’ da karin sautin sama da ‘manunin lokaci -nàà da kuma ‘suna xan aikatau’. Duba wannan jadawalin don ka ga tsarinsa:

Lokaci Na Yanzu Na I

| **Mai / Masu Magana** | **Wakilin Suna** | **Manunin lokaci** | **Suna Xan Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | i | nàà | rubutawa | ínàà rubutawa |
| Na biyu | ká | nàà | rubutawa | kánàà rubutawa |
| Ta biyu | kí | nàà | rubutawa | kínàà rubutawa |
| Na uku | yá | nàà | rubutawa | yánàà rubutawa |
| Ta uku | tá | nàà | rubutawa | tánàà rubutawa |
| Na farko jam’i | mú | nàà | rubutawa | múnàà rubutawa |
| Na biyu jam’i | kú | nàà | rubutawa | kúnàà rubutawa |
| Na uku jam’i | sú | nàà | rubutawa | súnàà rubutawa |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa manunin lokacin ‘lokaci na sabo iri xaya ne. Idan za ka ba da misali da zagin aikatau da ba a alaqanta shi da wani mai magana ba sai ka ce ‘ánàà rubutawa’.

### 3.2.5 Lokaci Na Yanzu Na II

‘Lokaci na yanzu na II’ nuni yake yi da aikin da yake gudana a halin da ake ciki. Abin da ya bambanta shi da ‘lokaci na yanzu na I’ shi ne ‘manunin lokaci kamar yadda za ka gani. Shi kuma ga yadda tsarinsa yake:

i. ‘wakilin suna’ da karin sautin sama
ii. ‘manunin lokaci -kèè
iii. ‘suna xan aikatau’.

Duba wannan jadawalin don ka ga tsarinsa haxe da misalai:

Lokaci Na Yanzu Na II

| **Mai / Masu Magana** | **Wakilin Suna** | **Manunin lokaci** | **Suna Xan Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | Ná | kèè | rubutawa | (ni ne)<br>nakee rubutawa |
| Na biyu | Ká | kèè | rubutawa | (kai ne)<br>kákèè rubutawa |
| Ta biyu | Kí | kèè | rubutawa | (ke ce)<br>kíkèè rubutawa |
| Na uku | Yá | kèè | rubutawa | (shi ne)<br>yákèè rubutawa |
| Ta uku | tá | kèè | rubutawa | (ita ce)<br>tákèè rubutawa |
| Na farko jam’i | mú | kèè | rubutawa | (mu ne)<br>múkèè rubutawa |
| Na biyu jam’i | Kú | kèè | rubutawa | (ku ne)<br>kúkèè rubutawa |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| Na uku jam'i | sú | kèè | rubutawa | (su ne)<br><br>súkèè rubutawa |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa manunin lokacin 'lokaci na yanzu na II iri xaya ne. Idan za ka ba da misali da zagin aikatau da ba a alaqanta shi da wani mai magana ba sai ka ce 'ákèè rubutawa'.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan ma'anar 'lokaci' da irin rawar da yake takawa a jimla. Na san cewa Hausatana da lokuta takwas. Na yi maka bayani kan zubi da tsarin 'shuxaxxen lokaci na I' da 'shuxaxxen lokaci na II' da 'lokaci na sabo' da 'lokaci na yanzu na I da kuma 'lokaci na yanzu na II.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- 'Lokaci' a nahawu shi ne sa'ar wanzar da aiki a jimla.
- Ka fahimci cewa Hausa tana da lokuta har guda takwas.
- Na yi maka bayani cewa kowane lokaci ana gane shi ta fuskar abu uku, su ne 'zagin aikatau ko wakilin suna' da manunin lokaci da kuma 'aikatau.
- Ka fahimci cewa 'lokaci na yanzu na I' da 'lokaci na yanzu na II' tsarinsu daban ne, suna zuwa da 'wakilin suna' da manunin lokaci da kuma 'suna xan aikatau'.
- Dangane da 'manunin lokaci' mun ga cewa 'shuxaxxen lokaci na I' da 'shuxaxxen lokaci na II ba su da 'manunin lokaci na bai xaya.

## Auna Fahimta

1. Bayyana hanyoyin da ake bi don fayyace lokaci?
2. Nuna kamanci da bambanci tsakanin lokaci na yanzu na I da na II?
3. Wace irin rawa manunin lokaci yake takawa a tsarin lokutan Hausa.

## 6.0 Jingar Aiki

1. Ta Wace hanya za ka bambance 'shuxaxxen lokaci na I da kuma na II?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 2 Lokutan Hausa II

Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Lokutan Hausa II
3.1.1 Lokaci Na Gaba Na I
3.1.2 Lokaci Na Gaba Na II
3.1.3 Umurtau / Wanin Lokaci
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

Wannan kashin zai yi xori ne a kan bayanin da na fara yi maka dangane da lokaci a nahawun Hausa. A kashin da ya gabata mun yi nazarin lokutan Hausa guda biyar daga cikin guda takwas da Hausa take da su. Yanzu wannan kashin zai kawo maka ragowar ukun, wato lokutan Hausa na II, wato 'lokaci na gaba na I' da 'lokaci na gaba na biyu' da kuma 'umurtau ko wanin lokaci. 'Lokaci' yana da matuqar muhimmanci a ilimin nahawu. Saboda in dai an yi maganar jimla to lallai a duba batu kan 'lokaci'.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce ka san:

- .zubi da tsarin lokutan Hausa na shida zuwa na takwas.

### 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Lokutan Hausa II

Wannan kashi zai yi maka bayani a kan lokutan Hausa aji na biyu. Lokutan Hausa kashi na biyu ya qunshi lokuta da suka haxa da ‘Lokaci Na Gaba Na I’ da ‘Lokaci Na Gaba Na II’ da kuma ‘Umurtau ko Wanin Lokaci’. Waxannan su ne lokutan da zan yi maka bayaninsu.

### 3.1.1 Lokaci Na Gaba Na I

Wannan nau’i ne na lokaci da yake nuni da cewa za a wanzar da wani aiki a wani lokaci mai zuwa da kuma tabbacin yin aikin. Wato, jimla tana xauke da wani aiki da za a yi shi nan gaba. ‘lokaci nag aba na xaya yana da zubi da tsari kamar haka:

i. manunin lokaci *záá*
ii. zagin aikatau (da karin sautin sama)
iii. aikatau

Duba wannan jadawalin domin ka ga tsarinsa haxe da misalai:

Lokaci Na Gaba Na I

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | Nà | záá | rubuta | záá nà (zan) rubuta |
| Na biyu | Kà | záá | rubuta | záá kà rubuta |
| Ta biyu | Ki | záá | rubuta | záá kí rubuta |
| Na uku | Yà | záá | rubuta | záá yà (zai) rubuta |
| Ta uku | tà | záá | rubuta | záá tà rubuta |
| Na farko jam’i | mù | záá | rubuta | záá mù rubuta |
| Na biyu jam’i | Kù | záá | rubuta | záá kù rubuta |
| Na uku jam’i | sù | záá | rubuta | záá sù rubuta |

Idan ka yi nazarin wannan jadawali za ka fahimci cewa ‘lokaci na gaba na I’ yana da tsari na daban da sauran lokutan. A nasa tsarin ‘manunin lokaci’ ne yake fara zuwa kafin ‘zagin aikatau’. ‘Aikatau’ kamar a duk lokutan yana zuwa bayan ‘zagin aikatau. Idan ka duba misalan za ka ga cewa a tsari na mai magana na farko ‘záá nà’ za a iya takure ‘manunin lokaci da zagin aikatau xin su koma ‘*zan*’, an shafe wasalin ‘zagin aikatau’ kuma sai karin sautin ya koma faxau (wato karin sauti mai yin sama da kaifin murya kuma ya dawo qasa) *zân*.. Haka idan ka duba tsarin mai magana na uku *záá yà* ana iya shafe wasalin qarshe na zagin aikatau, da ma kuma wajen rubuta /y/ da sigar /i/ take bayyana, sai a samu *zai*. Haka kuma za a iya yin misali ba tare da an danganta da wani mai magana ba kamar a ce, ‘zá à rubuta’.

### 3.1.2 Lokaci Na Gaba Na II

Wannan nau’i ne na lokaci da yake nuni da cewa za a wanzar da wani aiki a wani lokaci mai zuwa amma kuma babu tabbacin yin aikin. Wato, jimla tana xauke da wani aiki da za a yi shi nan gaba maras tabbas. Ga yadda zubinsa yake:

i. zagin aikatau da karin sautin sama.
ii. manunin lokaci -à
iii. aikatau

Duba wannan jadawalin domin ka ga tsarinsa haxe da misalai:

Lokaci Na Gaba Na II

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | ná | à | rubuta | náà rubuta |
| Na biyu | ká | à | rubuta | káà rubuta |
| Ta biyu | kí | à | rubuta | kíà rubuta |
| Na uku | yá | à | rubuta | yáà rubuta |
| Ta uku | tá | à | rubuta | táà rubuta |
| Na farko jam’i | mú | à | rubuta | múà rubuta |
| Na biyu jam’i | kú | à | rubuta | kúà rubuta |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| Na uku jam'i | sú | à | rubuta | súà rubuta |

Idan ka yi nazarin misalan da suka zo a wannan jadawali za ka fahimci cewa 'lokaci na gaba na II' yana da tsari da karin sautin 'zagin aikatau' yake haxewa da karin sautin manunin lokaci su haifar da karin sauti faxau wajen lafazi kamar yadda ka gani a duk misalan. Wajen rubutu kuwa ana rubuta 'kia' da *kya* ne, 'mua' da *ma*, 'kua' da *kwa*, 'sua' kuma da *sa*. Haka kuma za a iya yin misali ba tare da an danganta da wani mai magana ba kamar a ce, 'áà rubuta'.

### 3.1.3 Umurtau

Wannan nau'i na lokaci da yake xauke da umarni a jimla. Shi 'umurtau' ba ya nuni da wani lokaci kamar yadda muka yi nazarin lokuta bakwai na baya. Wannan shi ne dalilin da wasu masana nahawun Hausa suke kiran sa da 'wanin lokaci' (Sani, 1999: 77). Shi ya sa Sani (1999) ya bayyana cewa lokutan Hausa bakwai ne da 'wanin lokaci' xaya. Duk hanyar dai aka bi za a samu takwas. Yaya tsarin umurtau yake? 'Umurtau' ko 'wanin lokaci' yana da tsari kamar haka:

i. zagin aikatau da karin sauti qasa
ii. aikatau

Umurtau ba shi da 'manunin lokaci' saboda shi ba lokaci yake fayyacewa ba. Wannan ma qarin dalili ne da wasu suka kira shi da 'wanin lokaci'. Yanzu ga tsarinsa zan kawo maka a wannan jadawalin haxe da misalai:

Umurtau

| **Mai / Masu Magana** | **Zagin Aikatau** | **Manunin lokaci** | **Aikatau** | **Misali** |
|---|---|---|---|---|
| Na farko | nà | - | rubuta | (ba ni) *nà rubuta* |
| Na biyu | kà | - | rubuta | (karvi) *kà rubuta* |
| Ta biyu | kì | - | rubuta | (karvi) *kì rubuta* |
| Na uku | yà | - | rubuta | (ba shi) *yà rubuta* |
| Ta uku | tà | - | rubuta | (ba ta) *tà rubuta* |
| Na farko jam'i | mù | - | rubuta | (ba mu) *mù rubuta* |
| Na biyu jam'i | kù | - | rubuta | (ku karva) *kù rubuta* |
| Na uku jam'i | sù | - | rubuta | (su karva) *sù rubuta* |

Wani misalin da ba ka gani a jadawalin ba shi ne na yin amfani da zagin aikatau da ba a danganta shi da wani mai magana ba kamar a ce 'à rubuta'.

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan ma'anar lokutan Hausa kashi na biyu. Na kawo maka bayanai kan lokutan Hausa guda uku da suka haxa da 'lokaci na gaba na I' da 'lokaci na gaba na II' da kuma 'umurtau' ko 'wanin lokaci. Kowanne na yi maka bayaninsa ta hanyar jadawali mai haxe da misalai.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- 'Lokaci na gaba na I' lokaci ne da za a wanzar da aiki nan gaba kuma da tabbacin yin aikin.
- Shi kuwa 'lokaci na gaba na II' shi ma qunshe yake da aikin da za a wanzar a gaba amma shi babu tabbacin yin sa.
- 'Lokaci na gaba na I' yana da tsari na daban, domin shi nasa tsarin 'manunin lokaci' yana zuwa kafin 'zagin aikatau'.
- 'Umurtau' tsarinsa daban ne, ba kamar sauran bas hi ba shi da 'manunin lokaci', shi ya sa ake iya kiran sa da 'wanin lokaci'.

## Auna Fahimta

1. Bayyana ra'ayinka dangane da 'umurtau' lokaci ne ko wanin lokaci?
2. Nuna kamanci da bambanci tsakanin lokaci na gaba na I da na gaba na II?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Me ya sa 'manunin lokaci' ya zo kafin 'zagin aikatau' a tsarin 'lokaci na gaba na I?

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 3 Li'irabin Jimla I

### Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Ma'anar Li'irabi
3.1.1 Bishiyar Li'irabi
3.2 Li'irabin Jimla Mai Aikatau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

### 1.0 Gabatarwa

A wannan kashi zan yi maka bayanin li'irabin jimla mai aikatau a nahawun Hausa. Ya kamata ka sani cewa li'rabi yana da matuqar muhimmanci a nahawun harshe. Li'irabi shi ne yake fito da bayanan jimla daki-daki, kuma li'irabi tafiya yake yi da bishiyarsa wadda ake kira 'bishiyar li'irabi' ko 'bishiyar Galadanci'. Duk nau'o'in jimlar Hausa za a iya nuna su ta hanyar li'irabi da bishiyarsa. Bugu da qari, sanin abin da ake nufi da li'irabi da bishyarsa shi zai qara nuna cewa ka fahimci rukunonin nahawun Hausa. Domin rukunonin nahawun Hausa da ka yi nazarin su a baya su ne ake qara nuna su a tsarin li'irabi da bishiyarsa. Hari la yau, li'irabi da bishiyarsa zai qara fito maka da dangantakar kalmomin da rukunonin nahawu. A wannan kashi zan gabatar maka da li'irabin jimlar Hausa aji na farko inda za mu yi li'irabin jimlar Hausa masu xauke da aikatau.

### 2.0 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi ana so ka fahimci:

- Abin da ake nufi da li'rabi.
- Bishiyar li'irabi

- Li’rabin jimla mai aikatau

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Ma’anar Li’irabi

Li’rabi fannin nahawu ne da ya danganci yadda ake datsa jimla yanki-yanki da nuna ire-iren kalmomin da ke qunshe a cikin kowane yanki tare da bayyana halayyar kalmomin da dangantakarsu a cikin jimla (Zarruq, 1999: 90). Wasu masana nahawun Hausa sun kira li’irabi da ‘fixar jimla’, kamar Zarruq, 1999). A taqaice dai ‘li’irabi ko fixar jimla’ ya danganci yadda ake yayyanka jimla da nuna ire-iren rukunan nahawu da jimlar ta qunsa da kuma dangantakarsu. Misali, a yankin bayani akwai ‘aikatau’ da ‘wakilin suna ko zagin aikatau’ da kuma ‘aikatau’. A tsari na li’irabi ana taqaita rubuta rukunan nahawu ne, misali ‘yankin bayani’ sai a rubuta shi da YB (wato ‘yankin aikatau’ YA), ‘yankin suna’ a rubuta shi da YSN. Duba waxannan misalan:

Taqaita Rukunin Nahawu da cikakkensa

1a. J: Jimla
b. YSn: Yankin Suna
c. YB: Yankin Bayani
d. TA: Tawagar Aikatau
e. WS: Wakilin Suna
f. ZA: Zagin Aikatau
g. Ml: Manunin Lokaci
h. A: Aikatau
i. Qrf: Qarfafau
j. Sn: Suna
k. Byn: Bayanau
l. Mfy: Mafayyaci
m. Drk: Dirka
n. Mdg: Madanganci
o. Mhx: Mahaxi
p. M: Ma’auni
q. Sf: Sifa
r. Jkd: Jakada

Da sauransu.

Wani tsarin na ‘li’irabi’ shi ne idan an taqaita rukunin ana yin alamar kibiya a bayansa. Alamar kibiya tana nufin ‘abu yana zama’ wani abu. Misali, J → YSn + YB. Idan an yi alamar tarawa ana nufin abu yana iya zama abu biyu ko sama da haka. Yana daga cikin tsarin li’irabi a fara gabatar da rukuni mai ‘ya’ya kafin ‘ya’yan. Misali, dole a fara gabatar da ‘Tawagar Aikatau’ kafin a ambaci abubuwan da ya qunsa. Yayin da aka gama gabatar da kalmomin rukunan nahawu sai kuma a shiga tsarin rubuta kalmomin da suka dace da rukunan nahawu. Misali, A *kama*. Alamar a nan tana matsayin taqaita sunan ‘aikatau’. Li’irabi tare yake tafiya da ‘bishiyarsa’ wadda ake kira ‘bishiyar li’irabi’, wasu masana nahawun Hausa suna kiran ta da ‘bishiyar Galadanci’ (saboda M.K.M. Galadanci a littafinsa *Introduction to Hausa Grammar* ya kawo misalan bishiyar li’irabi da yawa, shi ya sa ake danganta bishiyar da Galadanci). Sashe na gaba zai gabatar maka da ‘bishiyar li’irabi’.

### 3.1.1 Bishiyar Li’irabi

Bayan an gabatar da li’irabi ko fixar jimla abu na gaba shi ne a fito da jimla a tsari na surar bishiya. ‘Bishiyar li’irabi’ kamar yadda Zarruq (2005: 91) tana bayyana dangantakar kalmomi. Amma fa kalmomin nan su ne rukunan nahawu, ka ga daidai ne a ce ‘bishiyar li’irabi’ tana bayyana dangantakar da ke tsakanin rukunan nahawu. A taqaice dai ‘bishiyar li’irabi tana nuna hoton jimla ne a tsari na surar bishiya kamar yadda za ka gani a sashe na 3.2.

## 3.2 Li’irabin Jimla Mai Aikatau

Tunda ka fahimci abin da ake nufi da li’irabi da kuma bishiyarsa, yanzu zan yi maka li’irabin jimla mai aikatau. Misali:

2. ‘Abdu ya tafi makaranta.

J → YSn + YB

YB → TA + YSn

TA → ZA + ML + A

ZA → yá-

ML → -á

A → tafi

YSn → Sn

Sn → Abdu, makaranta

Yanzu za mu yi amfani da bishiyar li’irabi don mu nuna li’irabin jimlar a sura ta biya. Duba misali na 3.

3




Tambaya a nan ita ce mene ne matsayin bishiyar li’irabi? Amsa dai ita ce a tsari na manufar nahawu, idan aka kawo samfuri (wato misali xaya), ana so ne ya kasance madubin da za a xora dukkan sauran misalan. Wannan shi ya sa misalin da na kawo maka a (3) zai zame maka samfurin da za ka samar da bishiyar li’irabi na duk wata jimla mai xauke da aikatau a nahawun Hausa. Abin da za ka kiyaye da shi shi ne duk manyan yankunan jimla, wato ‘yankin suna’ da ‘yankin bayani’ da na nuna maka a misali na (3) za a iya faxaxa kowanne. Wato, yankin suna mai makon ya xauki suna shi kaxai zai iya kasancewa kamar haka: ‘Wani xan gajeren yaro fari mai wayo’. Haka ma yankin bayani, domin shi zai iya xaukar wani yankin sunan da kuma bayanau. Domin samun qarin bayani da misalai masu yawa na li’irabin jimla mai aikatau da irin bishiyarsu sai ka duba Galadanci (1976) da Bagari (1986) da kuma Zarruq (2005).

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan ma'anar li'irabi da irin rawar da yake takawa a jimla. Na kuma yi maka bayanin bishiyar li'irabi. Na kawo maka li'irabin jimla mai aikatau da kuma bishiyarsa.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Li'rabi fannin nahawu ne da ya danganci yadda ake yanka jimla yanki-yanki da nuna ire-iren kalmomin da ke qunshe a cikin kowane yanki tare da bayyana halayyar kalmomin da dangantakarsu a cikin jimla.
- A tsari na li'irabi ana taqaita rubuta rukunan nahawu.
- Idan an taqaita rukuni a tsarin li'irabi ana yin alamar kibiya a bayansa. Alamar kibiya tana nufin 'abu yana zama' wani abu.
- Idan an yi alamar tarawa ana nufin abu yana iya zama abu biyu ko sama da haka.
- Yana daga cikin tsarin li'irabi a fara gabatar da rukuni mai 'ya'ya kafin 'ya'yan.
- Yayin da aka gama gabatar da kalmomin rukunan nahawu sai kuma a shiga tsarin rubuta kalmomin da suka dace da rukunan nahawu.
- Li'irabi tare yake tafiya da 'bishiyarsa' wadda ake kira 'bishiyar li'irabi', wasu masana nahawun Hausa suna kiran ta da 'bishiyar Galadanci'.
- 'Bishiyar li'irabi' tana bayyana dangantakar da ke tsakanin rukunan nahawu.

## Auna Fahimta

1. Me ka fahimta da 'li'irabi'?
2. A kan me za a iya cewa an gina 'bishiyar li'irabi'?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Kawo li'irabi da bishiyar li'irabin 'Wani mutum ya sayi mota ja jiya'.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.

## Kashi Na 4 Li'irabin Jimla II

## Abubuwan Da Suke Ciki

1.0 Gabatarwa
2.0 Manufar Darasi
3.0 Qunshiyar Darasi
3.1 Li'irabin Jimla II
3.1.1 Li'irabin Jimla Maras Aikatau
4.0 Kammalawa
5.0 Taqaitawa
Auna Fahimta
6.0 Jingar Aiki
7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Qarin Nazari

## 1.0 Gabatarwa

Wannan kashi zai yi maka bayanin li'irabin jimla maras aikatau. Li'irabin jimla maras aikatau tsarinta daban yake, saboda haka sanin yadda li'irabinta yake yana da muhimmanci. Ya kamata ka sani cewa li'rabi yana da matuqar muhimmanci a nahawun harshe. Li'irabi shi ne yake fito da bayanan jimla daki-daki, kuma li'irabi tafiya yake yi da bishiyarsa wadda ake kira 'bishiyar li'irabi' ko 'bishiyar Galadanci'. Duk nau'o'in jimla maras aikatau Hausa za a iya nuna su ta hanyar li'irabi da bishiyarsa. Bugu da qari, sanin abin da ake nufi da li'irabi da bishyarsa shi zai qara nuna cewa ka fahimci rukunonin nahawun Hausa da suka kevanta da jimla maras aikatau. Hari la yau, li'irabi da bishiyarsa zai qara fito maka da dangantakar kalmomin da suke bayyana a jimla maras aikatau. A wannan kashi zan gabatar maka da li'irabin jimlar Hausa aji na biyu inda za mu yi li'irabin jimlar Hausa wadda ba ta zuwa da aikatau.

## 2.0 Manufar Darasi

A qarshen wannan darasi ana so ka fahimci:

- Abin da ake nufi da li'rabi.
- Bishiyar li'irabi.
- Li'rabin jimla maras aikatau.

## 3.0 Qunshiyar Darasi

## 3.1 Li'irabin Jimla II

A wannan sashe zan kawo maka bayani kan li'irabin jimla aji na biyu. Li'irabin da za mu yi nazari shi ne na jimla maras aikatau. Ka dai rigaya ka san cewa jimla a Hausa ta kasu gida biyu, wadda take xauke da aikatau da kuma wadda ba ta zuwa da aikatau. Tunda mun yi bayanin cewa jimlolin Hausa suna da tsari na 'yankin suna' da 'yankin bayani'. Zan iya faxa maka cewa jimloli marasa aikatau an gina su ne kacokan a kan 'yankin suna'. Sashe na gaba zai kawo maka bayani a kan li'irabin jimla maras aikatau.

### 3.1.1 Li'irabin Jimla Maras Aikatau

A baya na yi maka bayanin cewa akwai jimloli masu yawa da ba sa zuwa da aikatau. Irin waxannan jimloli sun qunshi jimla dirkau da tambayau da kuma nunau. Tsarin li'irabinsu da na jimla mai aikatau duk iri xaya ne, domin duk suna da yankin suna da kuma yankin bayani. Bambancin kawai shi ne a tsarin li'irabin jimla maras aikatau babu 'aikatau' a yankin bayani. Saboda haka, tsarin li'irabinsu zai nuna maka cewa: J $\rightarrow$ YSn + YB. Li'irabin jimla maras aikatau shi ma tare yake tafiya da 'bishiyarsa' wadda ake kira 'bishiyar li'irabi'. 'Bishiyar li'irabi' kamar yadda Zarruq (2005: 91) tana bayyana dangantakar kalmomi. Amma fa kalmomin nan su ne rukunan nahawu, ka ga daidai ne a ce 'bishiyar li'irabi' tana bayyana dangantakar da ke tsakanin rukunan nahawu. A taqaice dai 'bishiyar li'irabi tana nuna hoton jimla ne a tsari na surar bishiya kamar yadda za ka gani nan gaba kaxan. Yanzu duba samfurin li'irabin jimla maras aikatau a misali na (1):

1. Wannan mota doguwa ce.

J $\rightarrow$ YSnn + YB

YSn $\rightarrow$ $Sft^1$ + $K^2$

$Sft^1$ $\rightarrow$ Nn

Nn → Wannan

$K^2$ → Sn

Sn → mota

YB → $Sft^3$ + Drk

$Sft^3$ → doguwa

Drk → ce

A nan ya kamata ka sani cewa kalmomin da suke zuwa kafin 'suna' ko a bayansa don su bayyana shi ko su faxi wani abu a kan sa ko su kwatanta / siffanta shi, to su ne ake kira da kalmomin 'sifatau'. Irin waxannan kalmomi su ne 'siffataccen suna'. Ka ga 'siffataccen suna' zai iya samun gurabe uku a cikin jimla (wannan ya shafi jimla mai aikatau ko maras aikatau). Idan ka yi nazarin wannan jimla za ka ga cewa 'wannan mota' YSn ne 'doguwa ce' kuma YB. Tunda jimlar ba ta da aikatau 'siffataccen suna' zai iya kasancewa a ko'ina kamar yadda za ka gani a bishiyar li'irabi. Yanzu za mu yi amfani da bishiyar li'irabi don mu nuna li'irabin jimlar. Duba misali na 2.

2




Wata hanyar ta yin li'irabin ita ce:

3. J → YSn + YB

YSn → Nn + Sn

Nn → Wannan

Sn → mota

YB → Sf + Drk

Sf → doguwa

Drk → ce

Yanzu kuma ga yadda bishiyar li'irabin za ta kasance:

2.




Tambaya a nan ita ce mene ne matsayin bishiyar li'irabi? Amsa dai ita ce a tsari na manufar nahawu, idan aka kawo samfuri (wato misali xaya), ana so ne ya kasance madubin da za a xora dukkan sauran misalan. Wannan shi ya sa misalin da na kawo maka a (2) zai zame maka samfurin da za ka samar da bishiyar li'irabi na duk wata jimla maras aikatau a nahawun Hausa. Misali, ka ga idan aka ce 'Abdu qwararren malami ne', sai ka ce 'Abdu' shi ne a YSn, 'qwararren malami ne' a YB. Domin samun qarin bayani da misalai masu yawa na li'irabin jimla mai aikatau da irin bishiyarsu sai ka duba Galadanci (1976) da kuma Zarruq (2005).

## 4.0 Kammalawa

A wannan kashi na yi maka bayani kan ma’anar li’irabi da irin rawar da yake takawa a jimla maras aikatau. Na kuma yi maka bayanin bishiyar li’irabi. Na kawo maka li’irabin jimla maras aikatau da kuma bishiyarsa.

## 5.0 Taqaitawa

A wannan kashi, ka fahimci cewa:

- Li’rabi fannin nahawu ne da ya danganci yadda ake yanka jimla yanki-yanki da nuna ire-iren kalmomin da ke qunshe a cikin kowane yanki tare da bayyana halayyar kalmomin da dangantakarsu a cikin jimla.
- A tsari na li’irabi ana taqaita rubuta rukunan nahawu.
- Idan an taqaita rukuni a tsarin li’irabi ana yin alamar kibiya a bayansa. Alamar kibiya tana nufin ‘abu yana zama’ wani abu.
- Idan an yi alamar tarawa ana nufin abu yana iya zama abu wani abu na rukunin nahawu.
- Yana daga cikin tsarin li’irabi a fara gabatar da rukuni mai ‘ya’ya kafin ‘ya’yan.
- Yayin da aka gama gabatar da kalmomin rukunan nahawu sai kuma a shiga tsarin rubuta kalmomin da suka dace da rukunan nahawu.
- Li’irabi tare yake tafiya da ‘bishiyarsa’ wadda ake kira ‘bishiyar li’irabi’, wasu masana nahawun Hausa suna kiran ta da ‘bishiyar Galadanci’.
- ‘Bishiyar li’irabi’ tana bayyana dangantakar da ke tsakanin rukunan nahawu.

## Auna Fahimta

1. Me ka fahimta da ‘li’irabin jimla maras aikatau?
2. Bayyana rawar da kalmar dirka take takawa a li’irabi da kuma bishiyarsa?

## 6.0 Jingar Aiki

1. Kawo li’irabi da bishiyar li’irabin ‘Abdu ma sarki ne’.

## 7.0 Manazarta Da Wasu Ayyukan Don Qarin Nazari


Amfani, Ahmed Halliru. Further Issues in the Formation of the Hausa Verb. Journal of the Linguistic Association of Nigeria. 10: 1-8, 2007.

Bagari, Dauda Muhammad. Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida, 1986.

Bello, Ahmadu. Sabon Nahawun Hausa. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2014.

Fagge, Usman Usaini. Hausa Language and Linguistics. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2012.

Galadanci, Muhammad Kabir Mahmud. An Introduction to Hausa Grammar. Ikeja: Longman, 1976.

Jinju, Muhammadu Hambali. Rayayyen Nahawun Hausa. Zaria: NNPC, 1980.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Plc, 1999.

Sani, Mu'azu Alhaji Zaria. Alfiyyar Mu'azu Sani 2: Ginin Jimlar Hausa a Waqe. Kano: Benchark Publishers Limited, 2009.

Skinner, Neil. A Grammar of Hausa. Zaria: NNPC, 1979.

Yusuf, Mukhtar Abdulqadir. Hausa Grammar: An Introduction. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited, 2011.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Aikatau A Nahawun Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 1990.

Zarruq, Rabi'u Muhammad. Bishiyar Li'irabi A Nazarin Jumlar Hausa. Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, 2005.